الجزء ١٩ الحزب ٣٧

۞ وَقَالَ ٱلَّذِينَ لَا يَرۡجُونَ لِقَآءَنَا لَوۡلَآ أُنزِلَ عَلَيۡنَا ٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ
أَوۡ نَرَىٰ رَبَّنَاۗ لَقَدِ ٱسۡتَكۡبَرُواْ فِيٓ أَنفُسِهِمۡ وَعَتَوۡ عُتُوّٗا كَبِيرٗا
٢١ يَوۡمَ يَرَوۡنَ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةَ لَا بُشۡرَىٰ يَوۡمَئِذٖ لِّلۡمُجۡرِمِينَ وَيَقُولُونَ
حِجۡرٗا مَّحۡجُورٗا ٢٢ وَقَدِمۡنَآ إِلَىٰ مَا عَمِلُواْ مِنۡ عَمَلٖ فَجَعَلۡنَٰهُ
هَبَآءٗ مَّنثُورًا ٢٣ أَصۡحَٰبُ ٱلۡجَنَّةِ يَوۡمَئِذٍ خَيۡرٞ مُّسۡتَقَرّٗا
وَأَحۡسَنُ مَقِيلٗا ٢٤ وَيَوۡمَ تَشَقَّقُ ٱلسَّمَآءُ بِٱلۡغَمَٰمِ وَنُزِّلَ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ
تَنزِيلًا ٢٥ ٱلۡمُلۡكُ يَوۡمَئِذٍ ٱلۡحَقُّ لِلرَّحۡمَٰنِۚ وَكَانَ يَوۡمًا عَلَى
ٱلۡكَٰفِرِينَ عَسِيرٗا ٢٦ وَيَوۡمَ يَعَضُّ ٱلظَّالِمُ عَلَىٰ يَدَيۡهِ يَقُولُ
يَٰلَيۡتَنِي ٱتَّخَذۡتُ مَعَ ٱلرَّسُولِ سَبِيلٗا ٢٧ يَٰوَيۡلَتَىٰ لَيۡتَنِي لَمۡ
أَتَّخِذۡ فُلَانًا خَلِيلٗا ٢٨ لَّقَدۡ أَضَلَّنِي عَنِ ٱلذِّكۡرِ بَعۡدَ إِذۡ جَآءَنِيۗ
وَكَانَ ٱلشَّيۡطَٰنُ لِلۡإِنسَٰنِ خَذُولٗا ٢٩ وَقَالَ ٱلرَّسُولُ يَٰرَبِّ
إِنَّ قَوۡمِي ٱتَّخَذُواْ هَٰذَا ٱلۡقُرۡءَانَ مَهۡجُورٗا ٣٠ وَكَذَٰلِكَ
جَعَلۡنَا لِكُلِّ نَبِيٍّ عَدُوّٗا مِّنَ ٱلۡمُجۡرِمِينَۗ وَكَفَىٰ بِرَبِّكَ هَادِيٗا
وَنَصِيرٗا ٣١ وَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ لَوۡلَا نُزِّلَ عَلَيۡهِ ٱلۡقُرۡءَانُ جُمۡلَةٗ
وَٰحِدَةٗۚ كَذَٰلِكَ لِنُثَبِّتَ بِهِۦ فُؤَادَكَۖ وَرَتَّلۡنَٰهُ تَرۡتِيلٗا ٣٢



**(21) Kafiran da basa fatan gamuwa da mu, kuma basa tsoron azabar mu suka ce: "Me ya hana Allah ya saukar mana da Mal'iku, su bamu labarin gaskiyar Annabi Muhammad (S.A.W), ko kuma mu ga Ubangijinmu qiri-qiri, shi ya bamu labarin hakan?!". Lallai girman kai ya kankama a zukatan waxannan, har ya hana su imani, kuma sun wuce gona da iri a kafirci da shisshigi da wannan zancen nasu!. (22) Ranar da kafirai za su yi ido huxu da Mala'iku a lokacin mutuwarsu, da lokacin zaman barzahu, da yayin da za a tayar da su, da yayin da za a koro su zuwa wurin hisabi, da yayin da za su shiga wuta –to babu wani albishir ga wani kafiri a waxannan wurare, savanin Muminai, kuma Mala'iku za su ce musu: "Haramun ne a gare ku ku samu wani albishir daga wurin Allah". (23) Mun nufi ayyukan da kafirai suka yi a duniya na xa'a da alheri, sai muka mayar da su, saboda vacinsu da rashin amfaninsu, saboda kafircinsu, kamar qurar da take tashi, wadda mai kallo yake ganinta tana shigowa a cikin hasken rana ta taga (Window). (24) Muminai 'yan Aljanna a wannan ranar, sune mafi alherin matsayi, da kyawun wajen hutu a lokacin barcin qailulansu a duniya, sama da kafirai, saboda imaninsu da Allah da kyawawan ayyukansu. (25) Ya kai wannan Manzo, ka ambaci ranar da sama za ta tsattsage, da fararen giza-gizai sirara, kuma za a sassaukar da Mala'iku zuwa filin taron alqiyama, saukarwa mai yawa, saboda suna da yawa.**

**(26) Mulki wanda yake shi ne mulki na gaske tabbatacce a ranar alqiyama na Allah ne mai rahama, tsarki ya tabbata gare shi. Kuma lallai wannan ranan mai wahala ce ga kafirai, savanin Muminai, rana ce mai sauki a gare su.**

**(27) Ka ambaci – Ya kai wannan Manzo- ranar da azzalumi zai cize yatsansa, don tsananin nadama, saboda qin biyayayya ga Manzon Allah (S.A.W), yana mai cewa: "Kaico na! Ina ma na bi Manzon Allah cikin abin da ya zo da shi daga Ubangijinsa, na xauki hanyar tsira tare da shi!".**

**(28) Zai ce saboda tsananin baqin ciki, ya na yin mummunan addu'ar halaka ga kansa yana cewa: "Kaico na! Da na sani da ban xauki kafiri wane a matsayin aboki ba!".**

**(29) Wannan abokin nawa kafiri ya vatar da ni daga hanyar Alqur'ani, bayan ya iso gare ni ta hanyar Manzon Allah. Kuma lallai Shaixan ya kasance mai yawan tavar da mutum ne, kuma idan ya faxa cikin baqin ciki sai barranta daga gare shi".**

**(30) A wannan rana Manzon Allah zai ce - yana mai kai koken halin mutanensa - yana cewa: "Ya Ubangijina, lallai mutanena da ka aike ni zuwa wurinsu, sun rabu da wannan Alqur'anin, sun qaurace masa".**

**(31) Kuma irin yadda ka gamu da cutarwa, da kawar da mutane daga tafarkinka a wurin mutanenka – Ya kai wannan Manzo- haka muka sanya wa kowane Annabi cikin waxanda suka gabace ka abokin gaba, cikin kangararrun mutanensa. Ubangijinka ya isa mai shiryar wa zuwa ga tafarkin gaskiya. Kuma ya isa mai bayar da nasara, wanda zai taimake ka a kan abokan gabarka". (32) Waxanda suka Kafirce wa Allah suka ce: "Ina ma an saukar wa da Manzo wannan Alqur'anin a jumlace, a lokaci guda, ba a saukar masa da shi a rarrabe ba. Mun sassaukar da Alqur'ani a rarrabe domin mu tabbatar maka da zuciyarka – Ya kai wannan Manzo- ta hanyar saukar da shi lokaci bayan lokaci. Mun saukar da shi kaxan kaxan ne domin sauwaqe fahimtarsa da hardarsa.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Kafirci yana hana karvar ayyuka nagartattu. 2 - Haxarin munanan abokai. 3 - Cutarwar da take cikin qauracewa Alqur'ani. 4 - Yana daga cikin hikimomin saukar da Alqur'ani a rarrabe, kwantar wa da Annabi (S.A.W) da hankalinsa, da sauwaqe fahimtarsa, da haddarsa, da aiki da shi.**

وَلَا يَأۡتُونَكَ بِمَثَلٍ إِلَّا جِئۡنَٰكَ بِٱلۡحَقِّ وَأَحۡسَنَ تَفۡسِيرًا
٣٣ ٱلَّذِينَ يُحۡشَرُونَ عَلَىٰ وُجُوهِهِمۡ إِلَىٰ جَهَنَّمَ أُوْلَٰٓئِكَ
شَرّٞ مَّكَانٗا وَأَضَلُّ سَبِيلٗا ٣٤ وَلَقَدۡ ءَاتَيۡنَا مُوسَى ٱلۡكِتَٰبَ
وَجَعَلۡنَا مَعَهُۥٓ أَخَاهُ هَٰرُونَ وَزِيرٗا ٣٥ فَقُلۡنَا ٱذۡهَبَآ
إِلَى ٱلۡقَوۡمِ ٱلَّذِينَ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِنَا فَدَمَّرۡنَٰهُمۡ تَدۡمِيرٗا ٣٦
وَقَوۡمَ نُوحٖ لَّمَّا كَذَّبُواْ ٱلرُّسُلَ أَغۡرَقۡنَٰهُمۡ وَجَعَلۡنَٰهُمۡ لِلنَّاسِ
ءَايَةٗۖ وَأَعۡتَدۡنَا لِلظَّٰلِمِينَ عَذَابًا أَلِيمٗا ٣٧ وَعَادٗا وَثَمُودَاْ
وَأَصۡحَٰبَ ٱلرَّسِّ وَقُرُونَۢا بَيۡنَ ذَٰلِكَ كَثِيرٗا ٣٨ وَكُلّٗا
ضَرَبۡنَا لَهُ ٱلۡأَمۡثَٰلَۖ وَكُلّٗا تَبَّرۡنَا تَتۡبِيرٗا ٣٩ وَلَقَدۡ أَتَوۡاْ عَلَى
ٱلۡقَرۡيَةِ ٱلَّتِيٓ أُمۡطِرَتۡ مَطَرَ ٱلسَّوۡءِۚ أَفَلَمۡ يَكُونُواْ يَرَوۡنَهَاۚ
بَلۡ كَانُواْ لَا يَرۡجُونَ نُشُورٗا ٤٠ وَإِذَا رَأَوۡكَ إِن يَتَّخِذُونَكَ
إِلَّا هُزُوًا أَهَٰذَا ٱلَّذِي بَعَثَ ٱللَّهُ رَسُولًا ٤١ إِن كَادَ
لَيُضِلُّنَا عَنۡ ءَالِهَتِنَا لَوۡلَآ أَن صَبَرۡنَا عَلَيۡهَاۚ وَسَوۡفَ
يَعۡلَمُونَ حِينَ يَرَوۡنَ ٱلۡعَذَابَ مَنۡ أَضَلُّ سَبِيلًا ٤٢ أَرَءَيۡتَ
مَنِ ٱتَّخَذَ إِلَٰهَهُۥ هَوَىٰهُ أَفَأَنتَ تَكُونُ عَلَيۡهِ وَكِيلًا ٤٣



**(33) Ya kai wannan Manzo- Mushirikai ba za su tava iya kawo wani misali ba, a kan abubuwan da suke ba da shawara a kansu, amma dai mun zo maka da amsa ta gaskiya, kuma mun zo maka bayanin da ya fi kyau.**

**(34) Waxanda za a kora su ranar alqiyama, ana jansu a kan fuskokinsu zuwa wutar Jahannama, su ne masu mafi munin wurin zama, domin wurin zamansu shi ne Jahannama, kuma su ne suka fi kowa nisa daga tafarkin gaskiya, domin tafarkinsu tafarkin kafirci ne da vata.**

**(35) Haqiqa mun ba wa Annabi Musa (A.S) littafin Attaura, kuma mun mayar da xan'uwansa Annabi Haruna (A.S) Manzo tare da shi, domin ya kasance mataimaki a gare shi.**

**(36) Sai muka ce musu (su biyun): "Ku tafi wurin Fir'auna da mutanensa, waxanda suka qaryata ayoyinmu". Sai suka bi umarnin mu, suka tafi wurinsu, suka kira su zuwa ga kaxaita Allah da bauta (Wato tauhidi), sai mutanen suka qaryata su, sai muka halakar da su, halakarwa mai tsanani.**

**(37) Mutanen Annabi Nuhu yayin da suka qaryata Annabi Nuhu (A.S) Mun halakar da su, da nutsar da su cikin teku, muka sanya halakar da su dalili ne da yake nuna ikon mu wajen tumbuke azzalumai. Kuma mun tanadar wa azzalumai azaba mai ciwo a ranar alqiyama.**

**(38) Mun halakar da Adawa, mutanen Annabi Hudu da Samudawa mutanen Annabi Salihu, da Ma'abota rijiya, da al'ummu masu yawan tsakanin waxannan al'ummu uku xin.**

**(39) Dukkan waxannan da aka halakar sai da muka buga musu misali da halakawar da muka yi wa al'ummun da suka gabata, da dalilan da suka sa, don su wa'azantu, kuma dukkanin su mun halakar da su da, halakarwa mai tsanani, saboda kafircinsu da taurin kansu.**

**(40) Haqiqa mutanenka masu qaryata Annabawa sun je alqaryar mutanen Annabi Lux – a hanyarsu ta zuwa qasar Sham-, wadda aka yi mata ruwan duwatsu, a matsayin uquba a kan aikata alfasha, domin su dauki izina. Shin sun makance ne?, ba su ga wannan alqaryar ba? A'a. Bari dai, su ba sa qaddara yiwuwar wani tashi ne bayan mutuwa, da za a yi musu hisabi bayansa.**

**(41) Idan waxannan masu qaryata tashin alqiyama sun gamu da kai – Ya kai wannan Manzo- sai su yi maka izgili suna cewa don izgilanci da inkari: "Wannan shi ne wanda Allah ya aiko shi a matsayin Manzo zuwa wurin mu?!".**

**(42) Tabbas ya kusa ya kawar da mu daga bautar abubuwan bautar mu, ba don mun yi haquri kan bautarsu ba, ai da ya kawar da mu daga gare su da hujjojinsa da dalilansa. Kuma da sannu zasu sani, a yayin da zasu ga azaba a cikin qaburburansu, da kuma ranar alqiyama, waye wanda ya fi vata daga tafarkin gaskiya, su ko shi?! Kuma da sannu zasu san waye mafi vata a cikinsu.**

**(43) Ya kai wannan Manzo- ka ga wanda ya xauki son zuciyarsa abin bautarsa, yana yi masa biyayya, yanzu kai zaka iya zama mai kiyaye shi, har ka mayar da shi zuwa ga imani, ka hana shi kafirci?!".**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Kafirce wa Allah da qaryata ayoyinsa sababi ne na halakar da al'ummu.**
**2 - Rshin imani da tashin alqiyama sababi ne na rashin xaukan wa'azi.**
**3 - Izgilanci ga masu gaskiya sha'anin kafirai ne.**
**4 - Haxarin bin son zuciya.**

أَمۡ تَحۡسَبُ أَنَّ أَكۡثَرَهُمۡ يَسۡمَعُونَ أَوۡ يَعۡقِلُونَۚ إِنۡ هُمۡ إِلَّا
كَٱلۡأَنۡعَٰمِ بَلۡ هُمۡ أَضَلُّ سَبِيلًا ٤٤ أَلَمۡ تَرَ إِلَىٰ رَبِّكَ كَيۡفَ مَدَّ
ٱلظِّلَّ وَلَوۡ شَآءَ لَجَعَلَهُۥ سَاكِنٗا ثُمَّ جَعَلۡنَا ٱلشَّمۡسَ عَلَيۡهِ دَلِيلٗا
٤٥ ثُمَّ قَبَضۡنَٰهُ إِلَيۡنَا قَبۡضٗا يَسِيرٗا ٤٦ وَهُوَ ٱلَّذِي جَعَلَ لَكُمُ
ٱلَّيۡلَ لِبَاسٗا وَٱلنَّوۡمَ سُبَاتٗا وَجَعَلَ ٱلنَّهَارَ نُشُورٗا ٤٧ وَهُوَ
ٱلَّذِيٓ أَرۡسَلَ ٱلرِّيَٰحَ بُشۡرَۢا بَيۡنَ يَدَيۡ رَحۡمَتِهِۦۚ وَأَنزَلۡنَا مِنَ
ٱلسَّمَآءِ مَآءٗ طَهُورٗا ٤٨ لِّنُحۡـِۧيَ بِهِۦ بَلۡدَةٗ مَّيۡتٗا وَنُسۡقِيَهُۥ
مِمَّا خَلَقۡنَآ أَنۡعَٰمٗا وَأَنَاسِيَّ كَثِيرٗا ٤٩ وَلَقَدۡ صَرَّفۡنَٰهُ بَيۡنَهُمۡ
لِيَذَّكَّرُواْ فَأَبَىٰٓ أَكۡثَرُ ٱلنَّاسِ إِلَّا كُفُورٗا ٥٠ وَلَوۡ شِئۡنَا
لَبَعَثۡنَا فِي كُلِّ قَرۡيَةٖ نَّذِيرٗا ٥١ فَلَا تُطِعِ ٱلۡكَٰفِرِينَ وَجَٰهِدۡهُم
الحزب ٣٧ بِهِۦ جِهَادٗا كَبِيرٗا ٥٢ ۞ وَهُوَ ٱلَّذِي مَرَجَ ٱلۡبَحۡرَيۡنِ هَٰذَا
عَذۡبٞ فُرَاتٞ وَهَٰذَا مِلۡحٌ أُجَاجٞ وَجَعَلَ بَيۡنَهُمَا بَرۡزَخٗا
وَحِجۡرٗا مَّحۡجُورٗا ٥٣ وَهُوَ ٱلَّذِي خَلَقَ مِنَ ٱلۡمَآءِ بَشَرٗا فَجَعَلَهُۥ
نَسَبٗا وَصِهۡرٗاۗ وَكَانَ رَبُّكَ قَدِيرٗا ٥٤ وَيَعۡبُدُونَ مِن دُونِ ٱللَّهِ
مَا لَا يَنفَعُهُمۡ وَلَا يَضُرُّهُمۡۗ وَكَانَ ٱلۡكَافِرُ عَلَىٰ رَبِّهِۦ ظَهِيرٗا ٥٥



**(44) Bari dai! Shin – Ya kai wannan Manzo- kana zaton cewa mafiya yawan waxanda kake kiransu zuwa kaxaita Allah, da biyayya a gare shi, suna sauraronka, sauraron karvar gaskiya? ko suna hankaltar dalilai da hujjoji?! Ai su ba komai ba ne facekamar dabbobi suke, wajen ji da hankalta da fahimta, kai sun ma fi dabbobi vata da rashin kan gado.**

**(45) Baka gani ba – Ya kai wannan Manzo - alamomin halittar Allah, yayin da ya shimfixa inuwa a bayan qasa, wanda da ya so, ya bar ta a daskare, bata motsi da ya sanya ta hakan, sannan muka sanya rana tana nuna inuwar, ta yi tsayi ko ta yi gajarta.**

**(46) Sannan sai mu kame inuwar, ta hanyar rage ta kaxan kaxan, gwargwadon xagawar rana.**

**(47) Allah shi ne wanda ya sanya muku dare a matsayin tufafi, yana suturta ku, kuma yana suturta sauran abubuwa. Kuma shi ne wanda ya sanya muku barci a matsayin hutu, kuna hutawa da shi daga shagulgulanku. Kuma shi ne wanda ya sanya muku yini a matsayin lokacin da kuke fita zuwa ga ayyukan ku.**

**(48) Shi ne wanda yake aiko da iska, tana yin albishir da saukowar ruwan sama, wanda yana xaya daga cikin rahamar Ubangiji ga bayinsa. Mun saukar da ruwa mai tsarki daga sama, kuna yin tsarki da shi.**

**(49) Don mu raya qasar da ta qeqashe da wannan ruwan da ya sauka, qasar da babu wani tsiro a kanta, ta hanyar fitar da tsirrai kala-kala, da yaxa yabanya a bayan ta, kuma don a shayar da abin da muka halitta na dabbobin ni'ima da mutane da yawa, da wannan ruwan da ya sauka.**

**(50) Tabbas haqiqa mun yi bayani, mun bayyana hujjoji kala-kala a cikin Alqur'ani don su yi izna da su, amma sai mafiya yawan mutane suka qi, sai dai kafirce wa gaskiya da kangare mata.**

**(51) Da mun ga dama da mun aiko wa kowace alqarya da Manzo, wanda zai yi musu gargaxi, ya tsoratar da su daga uqubar Allah, amma bamu ga damar yin hakan ba, kawai dai mun aiko da Annabi Muhammad ya zama Manzo zuwa ga mutane gaba xaya.**

**(52) Don haka kar ka bi kafirai cikin abin da suke nemanka da shi, na yi musu sassauci, da abin da suka kawo na shawarwari. Ka yi jihadi a kansu da wannan Alqur'ani da aka saukar maka, ta hanyar haquri da cutarwar su, da xaukar wahala wajen kiransu zuwa ga Allah.**

**(53) Allah tsarki ya tabbata a gare shi, shi ne wanda ya haxa tsakanin ruwan tekuna guda biyu, ya haxa mai daxi da mai gishiri, sannan ya sanya shamaki da kariya a tsakaninsu, wadda take hana su haxuwa da juna.**

**(54) Shi ne wanda ya halicci mutum daga maniyyyin mace da na namiji, ya sanya alaqar kusanci da alaqar surukuntaka. Ubangijinka – Ya kai wannan Manzo- mai iko ne, babu abin da yake gagararsa, daga cikin ikonsa ne ya halicci mutum daga maniyin namiji da mace.**

**(55) Kafirai suna bauta wa gumaka, koma bayan Allah, gumakan da ba zasu amfane su ba, in sun yi musu biyayya, kuma baza su cutar da su ba, in sun sava musu. Lallai kafiri ya kasance mai bin Shaixan ne cikin abin da zai jawo masa fushin Allah mai tsarki.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Qasqantar kafiri zuwa ga wani matsayi, wanda bai kai matsayin dabbobi ba, saboda kafircewar sa ga Allah.**

**2 - Inuwa wata alama ce cikin alamomi masu nuna ikon Allah.**

**3 - Bambanta dalilai da hujjoji hanya ce mai kyau wajen tarbiyya.**

**4 - Yin kira da Alqur'ani xaya ne daga cikin fuskoki jihadi don xaukaka kalmar Allah.**

وَمَآ أَرۡسَلۡنَٰكَ إِلَّا مُبَشِّرٗا وَنَذِيرٗا ٥٦ قُلۡ مَآ أَسۡـَٔلُكُمۡ عَلَيۡهِ
مِنۡ أَجۡرٍ إِلَّا مَن شَآءَ أَن يَتَّخِذَ إِلَىٰ رَبِّهِۦ سَبِيلٗا ٥٧ وَتَوَكَّلۡ
عَلَى ٱلۡحَيِّ ٱلَّذِي لَا يَمُوتُ وَسَبِّحۡ بِحَمۡدِهِۦۚ وَكَفَىٰ بِهِۦ
بِذُنُوبِ عِبَادِهِۦ خَبِيرًا ٥٨ ٱلَّذِي خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ
وَمَا بَيۡنَهُمَا فِي سِتَّةِ أَيَّامٖ ثُمَّ ٱسۡتَوَىٰ عَلَى ٱلۡعَرۡشِۖ ٱلرَّحۡمَٰنُ
فَسۡـَٔلۡ بِهِۦ خَبِيرٗا ٥٩ وَإِذَا قِيلَ لَهُمُ ٱسۡجُدُواْۤ لِلرَّحۡمَٰنِ قَالُواْ
سَجۡدَة وَمَا ٱلرَّحۡمَٰنُ أَنَسۡجُدُ لِمَا تَأۡمُرُنَا وَزَادَهُمۡ نُفُورٗا۩ ٦٠ تَبَارَكَ
ٱلَّذِي جَعَلَ فِي ٱلسَّمَآءِ بُرُوجٗا وَجَعَلَ فِيهَا سِرَٰجٗا وَقَمَرٗا
مُّنِيرٗا ٦١ وَهُوَ ٱلَّذِي جَعَلَ ٱلَّيۡلَ وَٱلنَّهَارَ خِلۡفَةٗ لِّمَنۡ أَرَادَ
أَن يَذَّكَّرَ أَوۡ أَرَادَ شُكُورٗا ٦٢ وَعِبَادُ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلَّذِينَ يَمۡشُونَ
عَلَى ٱلۡأَرۡضِ هَوۡنٗا وَإِذَا خَاطَبَهُمُ ٱلۡجَٰهِلُونَ قَالُواْ سَلَٰمٗا
٦٣ وَٱلَّذِينَ يَبِيتُونَ لِرَبِّهِمۡ سُجَّدٗا وَقِيَٰمٗا ٦٤ وَٱلَّذِينَ
يَقُولُونَ رَبَّنَا ٱصۡرِفۡ عَنَّا عَذَابَ جَهَنَّمَۖ إِنَّ عَذَابَهَا كَانَ
غَرَامًا ٦٥ إِنَّهَا سَآءَتۡ مُسۡتَقَرّٗا وَمُقَامٗا ٦٦ وَٱلَّذِينَ إِذَآ
أَنفَقُواْ لَمۡ يُسۡرِفُواْ وَلَمۡ يَقۡتُرُواْ وَكَانَ بَيۡنَ ذَٰلِكَ قَوَامٗا ٦٧



**56 Ba mu aiko ka ba – Ya kai wannan Manzo-**
**sai don ka zama mai yin albishir ga wanda ya yi**
**biyayya ga Allah da imani da aiki nagari, kuma**
**mai gargaxi ga wanda ya sava masa da kafirci da**
**savo. 57 Ka ce musu – Ya kai wannan Manzo-::Ni**
**ba na neman wani lada a wurinku a sakamakon**
**isar da saqon Allah, sai dai wanda ya ga dama**
**daga cikinku, ya kama hanyar neman yardar**
**Allah ta hanyar ciyarwa, to ya yi". 58 Ya kai**
**wannan Manzon ka dogara ga Allah rayayye,**
**wanzazze, wanda baya mutuwa a cikin dukkan**
**al'amuranka, kuma ka tsarkake shi, kana mai**
**yabo a gare shi, tsarki ya tabbata a gare shi.**
**Ubangiji ya isa masani mai bada labari ga dukkan**
**zunuban bayinsa, babu abin da yake vuya a gare**
**shi, kuma da sannu zai yi musu sakayya a kai.**
**59 Wanda ya halicci sammai da qassai da abin**
**da ke tsakaninsu a kwanaki shida, sannan ya**
**xaukaka a kan Al'arshi, irin xaukakar da ta dace**
**da girmansa, shi ne mai rahama. Ya kai wannan**
**Manzo ka tambayi wanda ya san shi, shi ne Allah**
**wanda ya san komai, babu abin da yake vuya a**
**a gare shi. 60 Idan aka ce wa Kafirai: "Ku yi**
**sujjada ga Allah mai rahama". Sai su ce: "Ba zamu**
**yi sujjada ga mai rahamar ba, wane ne kuma mai**
**rahama (Ar-Rahmanu)?!, bamu san shi ba, bamu**
**yarda da shi ba, Yanzu zamu yi sujjada ga wanda**
**kake umarnin mu yi masa sujjada, alhali mu**
**bamu san shi ba". Sai umarnin su yi masa sujjada**
**ya sa suka qara nesa daga imani da Allah.**
**61 Alherin Allah ya yawaita, wanda ya sanya wa**
**taurarin da suke tsaye a wuri xaya da masu tafiya**
**masaukai, kuma ya sanya rana a sama, tana watso haske, kuma ya sanya wata a cikinta, yana haskaka bayan qasa,**
**da abin da yake samowa daga hasken rana. 62 Allah shi ne wanda ya sanya dare da yini suna maye gurbin juna,**
**xaya yana bin xayan, ya sanya su haka, don duk wanda yake son ya yi la'akari da ayoyin Allah ya shiryu, ko yake**
**son ya gode wa Allah a kan ni'imominsa. Yayin da Allah ya ambaci kafirai masu bijirewa imani da Allah da biyayya**
**a gare shi, a cikin wannan Surar, sai kuma ya ambaci siffofin bayinsa nagari, masu fuskantar xa'a gare shi, ya ce:**
**63 Bayin Allah mai rahama muminai, waxanda suke tafiya a bayan qasa cikin natsuwa da qanqan-da-kai, kuma**
**idan jahilai suka yi musu magana, ba sa fuskantarsu da irin wautar su. Suna faxa musu magana mai kyau ne, basa**
**musu wauta. 64 Waxanda suke kwana suna masu sujjada a kan fuskokinsu ga Ubangijinsu, suna masu tsayuwa**
**a kan qafafuwansu suna yin salla don Allah. 65 Waxanda suke faxa cikin addu'arsu ga Ubangijinsu, suna cewa:**
**"Ya Ubangijinmu, ka nesantar da mu daga azarbar wutar Jahannama. Lallai azabar Jahannama mai wanzuwa ce,**
**ga wanda ya mutu yana kafiri. 66 Haqiqa ta yi muni a matsayin wurin zama ga duk wanda ya tabbata a cikinta,**
**kuma ta yi muni a matsayin mazauni ga wanda zai zauna a cikinta.**
**67 Waxanda idan sun bayar da dukiyoyinsu, basa kaiwa zuwa ga almubazzaranci wacen bayarwar, kuma ba sa**
**yin qwauro wajen bayar da su, ga waxanda ya wajaba a ba su, kansu za su ba, ko waninsu. Don haka ciyarwarsu**
**ta kasance ne tsaka-tsakiya, ba almubazzaranci da qwauro, wato daidai wa daida da kuma adalci.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Mai kira zuwa ga Allah baya neman sakamako daga wurin mutane. 2 - Tabbatar da siffar xaukaka (istiwa'i) ga Allah, gwargwadon yadda ya dace da shi, mai tsarki da xaukaka. 3 - Sunan Ar-Rahman yana daga cikin sunayen Allah, wanxanda wani baya tarayya da shi a cikinsu, yana kuma nuni ga wata siffa daga cikin siffofin Allah, ita ce jinqai. 4 - Taimakon bawa ta hanyar maimaituwar yini da dare, domin ya riski abin da ya kuvuce masa na biyayya a xaya daga cikinsu.**
**5 - Yana daga cikin siffofin bayin Allah mai rahama, kasancewarsu masu qanqan-da-kai da haquri, da biyayya ga Allah a lokacin rafkanuwar mutane, da tsoron Allah, da lizimtar daidaito cikin ciyarwa da bayar da dukiya da sauran a'alamura.**

وَٱلَّذِينَ لَا يَدۡعُونَ مَعَ ٱللَّهِ إِلَٰهًا ءَاخَرَ وَلَا يَقۡتُلُونَ ٱلنَّفۡسَ
ٱلَّتِي حَرَّمَ ٱللَّهُ إِلَّا بِٱلۡحَقِّ وَلَا يَزۡنُونَۚ وَمَن يَفۡعَلۡ ذَٰلِكَ
يَلۡقَ أَثَامٗا ٦٨ يُضَٰعَفۡ لَهُ ٱلۡعَذَابُ يَوۡمَ ٱلۡقِيَٰمَةِ وَيَخۡلُدۡ
فِيهِۦ مُهَانًا ٦٩ إِلَّا مَن تَابَ وَءَامَنَ وَعَمِلَ عَمَلٗا صَٰلِحٗا
فَأُوْلَٰٓئِكَ يُبَدِّلُ ٱللَّهُ سَيِّـَٔاتِهِمۡ حَسَنَٰتٖۗ وَكَانَ ٱللَّهُ
غَفُورٗا رَّحِيمٗا ٧٠ وَمَن تَابَ وَعَمِلَ صَٰلِحٗا فَإِنَّهُۥ يَتُوبُ
إِلَى ٱللَّهِ مَتَابٗا ٧١ وَٱلَّذِينَ لَا يَشۡهَدُونَ ٱلزُّورَ وَإِذَا مَرُّواْ
بِٱللَّغۡوِ مَرُّواْ كِرَامٗا ٧٢ وَٱلَّذِينَ إِذَا ذُكِّرُواْ بِـَٔايَٰتِ
رَبِّهِمۡ لَمۡ يَخِرُّواْ عَلَيۡهَا صُمّٗا وَعُمۡيَانٗا ٧٣ وَٱلَّذِينَ يَقُولُونَ
رَبَّنَا هَبۡ لَنَا مِنۡ أَزۡوَٰجِنَا وَذُرِّيَّٰتِنَا قُرَّةَ أَعۡيُنٖ وَٱجۡعَلۡنَا
لِلۡمُتَّقِينَ إِمَامًا ٧٤ أُوْلَٰٓئِكَ يُجۡزَوۡنَ ٱلۡغُرۡفَةَ بِمَا صَبَرُواْ
وَيُلَقَّوۡنَ فِيهَا تَحِيَّةٗ وَسَلَٰمًا ٧٥ خَٰلِدِينَ فِيهَاۚ
حَسُنَتۡ مُسۡتَقَرّٗا وَمُقَامٗا ٧٦ قُلۡ مَا يَعۡبَؤُاْ بِكُمۡ رَبِّي
لَوۡلَا دُعَآؤُكُمۡۖ فَقَدۡ كَذَّبۡتُمۡ فَسَوۡفَ يَكُونُ لِزَامَۢا ٧٧

آياتها ٢٢٧ سُورَةُ الشُّعَرَاءِ ترتيبها ٢٦



**68 Waxanda basa kiran wani abin bauta tare da Allah (S.W.T), kuma basa kashe rai wadda Allah ya haramta a kashe ta, sai ta hanyar da Allah ya yi izini da ita, kamar a kashe wanda ya yi kisa, ko wanda ya yi ridda, ko magidancin da ya yi zina, kuma basa zina. Duk wanda ya yi waxannan manyan laifuka xin, to zai gamu da uqubar laifin da ya aikata a ranar alqiyama.**

**69 Za a ninka masa azaba a ranar alqiyama, kuma zai dauwama a cikin azabar yana wulaqantacce qasqantacce.**

**70 Sai dai wanda ya tuba zuwa ga Allah, ya yi imani, kuma ya aikata aiki nagari, wanda zai nuna gaskiyar tubansa, to waxannan Allah yana musanya laifukansu, su zama kyawawan ayyuka. Allah ya tabbata mai gafara ne ga zunubi, wanda ya tuba cikin bayinsu, kuma mai jin qai ne a gare su.**

**71 Duk wanda ya tuba zuwa ga Allah, kuma ya kafa hujja a kan tubansa da aiki nagari, da barin munanan ayyukan savo, to tubansa karvavviya ce.**

**72 Waxanda basa halartar wurin varna, kamar wuraren savo da shaqatawa na haramun, kuma idan suka wuce inda ake yin wargi da yasashshen zance da ayyuka, zai su wuce ba tare da tsayawa ba, suna masu girmama kawunansu, ta hanyar tsarkake kansu daga cuxanya da shi.**

**73 Waxanda idan aka tunatar da su da ayoyin Allah, na ji, da na gani, basa rufe kunnuwansu daga jin ayoyin da ake jin su, kuma basa makantar da idanuwansu daga ganin ayoyin da ake gani.**

**74 Waxanda suke faxa cikin addu'o'insu ga Ubangijinsu, suna cewa: "Ya Ubangijinmu, ka ba mu daga cikin matanmu, da 'ya'yan mu, waxanda zasu sanyaya mana idanuwan mu, saboda taqawarsu da daidaituwarsu a kan gaskiya, kuma ka sanya mu, mu zama jagorori ga masu taqawa, cikin gaskiya, ta inda za a yi koyi da mu.**

**75 Waxannan masu waxannan siffofin za a saka musu da xakuna maxaukaka a cikin Aljannar Firdausi, mafi xaukaka a cikin Aljannatai, saboda haqurinsu a kan biyayyar Allah, kuma za tarbe su da gaisuwa da aminci daga Mala'iku a cikinta, kuma zasu quvuta daga kowane irin aibi da cuta.**

**76 Zasu zauna a cikinta har abada, Madalla da ita a matsayin matabbata, da zasu tabbata a cikinta, da mazauni da zasu zauna a ciki.**

**77 Ya kai wannan Manzo ka ce wa kafirai masu dogewa a kan kafircinsu -: "Ubangijina bai damu da ku ba, saboda wani amfani da zai samu in kun masa biyayya, ba don yana da wasu bayi waxanda basa kiran wani wanda ba shi ba, kuma basa roqon wani, ba don su ba, da bai damu da ku ba. Haqiqa kun qaryata Manzo cikin abin da ya zo muku da shi daga wurin Ubangijinku, kuma tabbas sakamakon qaryatawa zai lazimce ku.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Karantarwa:

**1 - Yana daga cikin siffofin bayin Allah mai rahama, nesantar shirka, da kisan kai, ba tare da haqqi ba, da nesantar zina, da varna, da yin la'akari da ayoyin Allah da addu'a.**

**2 - Tuba na gaskiya yana wajabta barin savo da yin aikin xa'a.**

**3 - Haquri sababi ne na shiga Aljannar Firdausi, wadda ita ce mafi xaukaka a cikin Aljannatai.**

**4 - Wadatuwar Allah da rashin buqatarsa da imanin kafirai.**

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

ربع الحزب ٣٧
طسٓمٓ ١ تِلۡكَ ءَايَٰتُ ٱلۡكِتَٰبِ ٱلۡمُبِينِ ٢ لَعَلَّكَ بَٰخِعٞ نَّفۡسَكَ أَلَّا
يَكُونُواْ مُؤۡمِنِينَ ٣ إِن نَّشَأۡ نُنَزِّلۡ عَلَيۡهِم مِّنَ ٱلسَّمَآءِ ءَايَةٗ فَظَلَّتۡ
أَعۡنَٰقُهُمۡ لَهَا خَٰضِعِينَ ٤ وَمَا يَأۡتِيهِم مِّن ذِكۡرٖ مِّنَ ٱلرَّحۡمَٰنِ مُحۡدَثٍ
إِلَّا كَانُواْ عَنۡهُ مُعۡرِضِينَ ٥ فَقَدۡ كَذَّبُواْ فَسَيَأۡتِيهِمۡ أَنۢبَٰٓؤُاْ مَا كَانُواْ
بِهِۦ يَسۡتَهۡزِءُونَ ٦ أَوَلَمۡ يَرَوۡاْ إِلَى ٱلۡأَرۡضِ كَمۡ أَنۢبَتۡنَا فِيهَا مِن كُلِّ زَوۡجٖ
كَرِيمٍ ٧ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَةٗۖ وَمَا كَانَ أَكۡثَرُهُم مُّؤۡمِنِينَ ٨ وَإِنَّ
رَبَّكَ لَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلرَّحِيمُ ٩ وَإِذۡ نَادَىٰ رَبُّكَ مُوسَىٰٓ أَنِ ٱئۡتِ ٱلۡقَوۡمَ
ٱلظَّٰلِمِينَ ١٠ قَوۡمَ فِرۡعَوۡنَۚ أَلَا يَتَّقُونَ ١١ قَالَ رَبِّ إِنِّيٓ أَخَافُ
أَن يُكَذِّبُونِ ١٢ وَيَضِيقُ صَدۡرِي وَلَا يَنطَلِقُ لِسَانِي فَأَرۡسِلۡ
إِلَىٰ هَٰرُونَ ١٣ وَلَهُمۡ عَلَيَّ ذَنۢبٞ فَأَخَافُ أَن يَقۡتُلُونِ ١٤ قَالَ
كَلَّاۖ فَٱذۡهَبَا بِـَٔايَٰتِنَآۖ إِنَّا مَعَكُم مُّسۡتَمِعُونَ ١٥ فَأۡتِيَا فِرۡعَوۡنَ
فَقُولَآ إِنَّا رَسُولُ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ١٦ أَنۡ أَرۡسِلۡ مَعَنَا بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ
١٧ قَالَ أَلَمۡ نُرَبِّكَ فِينَا وَلِيدٗا وَلَبِثۡتَ فِينَا مِنۡ عُمُرِكَ سِنِينَ
١٨ وَفَعَلۡتَ فَعۡلَتَكَ ٱلَّتِي فَعَلۡتَ وَأَنتَ مِنَ ٱلۡكَٰفِرِينَ ١٩



# Suratush Shu'ara

An Saukar Da Ita A Makkah

## Daga Manufofin Surar:

**Fuskantar masu zarcewa a kan qaryata Manzon Allah (S.A.W), waxanda suke sukan saqon da ya zo da shi, da bayanin raunin sha'aninsu.**

## Tafsir

**(1) (Xaa Seen Mim): Bayani ya gabata dangane da ire-iren waxannan haruffa a farkon Suratul Baqara. (2) Waxancan ayoyin Alqur'ani ne, mai bayyana gaskiya daga qarya. (3) Mai yiwuwa ne – Ya kai wannan Manzo- saboda kwaxayinka da shiriyarsu, ka kashe kanka don baqin ciki da kwaxayin shiriyarsu. (4) In mun ga damar saukar musu da aya daga sama, to zamu saukar musu da ita, kuma za su miqa wuya gare ta cikin qanqan da kai, sai dai bamu ga damar hakan ba, don mu jarraba su, ko za su yi imani da gaibu?. (5) Kuma babu wani abin da zai zo wa waxannan Mushirikai na gargaxi, wanda yake sabon saukarwa ne daga Allah mai rahama, xauke da hujjoji akan kaxaita shi, da tabbatar da gaskiyar Annabinsa face sun kawar da kai daga jin sa da gasgata shi. (6) Tabbas sun qaryata abin da Manzonsu ya zo musu da shi, Kuma da sannu tabbacin abin da suka kasance suna izgili da shi zai zo musu, kuma azaba zata sauka a kansu. (7) Haka waxannan masu dogewa a kan kafircinsu zasu ci gaba a kan kafircinsu, ba za su kalli qasa ba, nau'ikan tsirrai kala nawa muka fitar da shi a cikinta, masu kyan kallo, masu yawan amfani?. (8) Lallai a cikin fitar da dangogin tsirrai kala-kala daga cikin qasa, akwai alamomi bayyanannu da suke nuna wanda ya fitar da su zai iya raya matattu, amma duk da haka mafi yawansu ba muminai ne ba. (9) Kuma lallai Ubangijinka -Ya kai wannan Manzo- shi ne mai rinjaye, babu mai iya rinjaye a kanshi, kuma mai jin qai ne ga bayinsa. (10) ka tuna – Ya kai wannan Manzo- yayin da Ubangijinka ya kira Annabi Musa (A.S) yana mai umartar sa da ya tafi wurin mutanen da suke azzalumai, saboda kafircinsu da Allah, da bautar da mutanen Annabi Musa da suke yi. (11) Su ne mutanen Fir'auna. Ya umarce su da tsoron Allah, ta hanyar kamanta umarninsa da nesantar haninsa, cikin tausasawa da sauqi. (12) Annabi Musa (A.S) ya ce: "Haqiqa ina jin tsoron su qaryata ni cikin abin da zan isar musu da shi daga gare ka". (13) Sai zuciyata ta yi qunci saboda qaryata ni da zasu yi, sai harshena ya kasa magana, don haka ka tura Mala'ika Jibrilu (A.S) zuwa xan 'uwa na Haruna, don ya zama mataimaki na. (14) Kuma ina da laifi a wurinsu saboda kashe bakibxe da na yi, don haka ina jin tsoron su kashe ni. (15) Sai Allah ya cewa Annabi Musa (A.S): "Ba zai yiwu ba! Baza su kashe ka ba, ka tafi, kai da xan uwanka Haruna, tare da ayoyinmu masu nuna gaskiyarku. Lallai muna tare da ku, da taimako da qarfafawa, muna jin abin da zaku faxa, da abin da za a faxa muku, babu wani abin da zai quvuce mana". (16) Ku tafi wurin Fir'auna, ku ce masa: "Mu biyun nan Manzani ne zuwa gare ka, daga wurin Ubangijin halitta gaba xaya". (17) "ka saki banu Isra'ila su tafi tare da mu". (18) Sai Fir'auna ya cewa Annabi Musa (A.S): Shin ba mu muka rene ka a wurin mu ba kana xan qarami, ka kuma zauna a cikinmu wasu shekaru a cikin rayuwarka, to mai ya kai ka yin iqrarin Annabci?" (19) "Kuma ka aikata babban abu yayin da ka kashe Bakibxe, don xaukar fansa ga wani mutum daga cikin mutanenka, ka zama cikin masu butulcin ni'imomin da na yi maka".**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Kwaxayin Manzon Allah (S.A.W) a kan shiriyar mutane. 2 - Tabbatar da siffar buwaya (Izza) da jin qai (Rahama) ga Allah. 3 - Muhimmanci yalwar qirji da fasahar zance ga mai kira zuwa ga Allah. 4 - Kiran Annabawa 'yantar da mutane ne daga bautar wanin Allah, zuwa ga bautawa Allah. 5 - Fir'auna ya kafa hujja a kan rashin yarda da Manzancin Annabi Musa da abin da ya faru na kisa, sai Annabi Musa ya tabbatar da faruwar hakan, wanda hakan yana nuna cewa kisan ba hujja ba ne na qaryata Annabi Musa da Fir'auna ya yi.**

قَالَ فَعَلۡتُهَآ إِذٗا وَأَنَا۠ مِنَ ٱلضَّآلِّينَ ٢٠ فَفَرَرۡتُ مِنكُمۡ لَمَّا خِفۡتُكُمۡ
فَوَهَبَ لِي رَبِّي حُكۡمٗا وَجَعَلَنِي مِنَ ٱلۡمُرۡسَلِينَ ٢١ وَتِلۡكَ نِعۡمَةٞ
تَمُنُّهَا عَلَيَّ أَنۡ عَبَّدتَّ بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ ٢٢ قَالَ فِرۡعَوۡنُ وَمَا رَبُّ ٱلۡعَٰلَمِينَ
٢٣ قَالَ رَبُّ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِ وَمَا بَيۡنَهُمَآۖ إِن كُنتُم مُّوقِنِينَ
٢٤ قَالَ لِمَنۡ حَوۡلَهُۥٓ أَلَا تَسۡتَمِعُونَ ٢٥ قَالَ رَبُّكُمۡ وَرَبُّ ءَابَآئِكُمُ
ٱلۡأَوَّلِينَ ٢٦ قَالَ إِنَّ رَسُولَكُمُ ٱلَّذِيٓ أُرۡسِلَ إِلَيۡكُمۡ لَمَجۡنُونٞ
٢٧ قَالَ رَبُّ ٱلۡمَشۡرِقِ وَٱلۡمَغۡرِبِ وَمَا بَيۡنَهُمَآۖ إِن كُنتُمۡ تَعۡقِلُونَ
٢٨ قَالَ لَئِنِ ٱتَّخَذۡتَ إِلَٰهًا غَيۡرِي لَأَجۡعَلَنَّكَ مِنَ ٱلۡمَسۡجُونِينَ
٢٩ قَالَ أَوَلَوۡ جِئۡتُكَ بِشَيۡءٖ مُّبِينٖ ٣٠ قَالَ فَأۡتِ بِهِۦٓ إِن كُنتَ
مِنَ ٱلصَّٰدِقِينَ ٣١ فَأَلۡقَىٰ عَصَاهُ فَإِذَا هِيَ ثُعۡبَانٞ مُّبِينٞ ٣٢
وَنَزَعَ يَدَهُۥ فَإِذَا هِيَ بَيۡضَآءُ لِلنَّٰظِرِينَ ٣٣ قَالَ لِلۡمَلَإِ حَوۡلَهُۥٓ
إِنَّ هَٰذَا لَسَٰحِرٌ عَلِيمٞ ٣٤ يُرِيدُ أَن يُخۡرِجَكُم مِّنۡ أَرۡضِكُم
بِسِحۡرِهِۦ فَمَاذَا تَأۡمُرُونَ ٣٥ قَالُوٓاْ أَرۡجِهۡ وَأَخَاهُ وَٱبۡعَثۡ فِي ٱلۡمَدَآئِنِ
حَٰشِرِينَ ٣٦ يَأۡتُوكَ بِكُلِّ سَحَّارٍ عَلِيمٖ ٣٧ فَجُمِعَ ٱلسَّحَرَةُ
لِمِيقَٰتِ يَوۡمٖ مَّعۡلُومٖ ٣٨ وَقِيلَ لِلنَّاسِ هَلۡ أَنتُم مُّجۡتَمِعُونَ ٣٩



**(20) Annabi Musa yace wa Fir'auna, yana mai tabbatarwa: "Na kashe mutmin ne yayin da nake cikin jahilai, gabanin wahayi ya zo mini".**
**(21) "Sai na gudu daga gare ku zuwa garin Madyana, bayan na kashe, yayin da na ji tsoron kar ku kashe ni, sai Ubangijina ya ba ni ilimi, kuma ya mayar da ni cikin Manzanninsa da yake aiko su zuwa ga mutane". (22) Kuma renonka da ka yi mini, ba tare da ka bautar da ni ba, duk da cewa kana bautar da Banu Isra'ila, wannan wata ni'ima ce wadda zaka iya yi min gorinta da gaskiya, amma wannan ba zai hana ni in kira ka zuwa ga Allah ba". (23) Sai Fir'auna ya cewa Annabi Musa (A.S): "To waye Ubangijin halittu, wadda kake riya cewa kai Manzonsa ne?!".**
**(24) Sai Annabi Musa (A.S) ya ce, yana mai bayar da amsa ga Fir'auna: "Ubangijin halittu, shi ne, Ubangijin Sammai da qassai, da abin da ke tsakaninsu. In har kun kasance masu sakankancewa ne da cewa shi ne Mahaliccinsu, to ku bauta masa". (25) Sai Fir'auna ya cewa waxanda suke gefensa cikin manyan mutanensa: "Bakwa jin amsar Musa, da abin da yake ciki na zancen qarya kuwa!". (26) Sai Annabi Musa ya ce musu: "Allah shi ne Ubangijinku, kuma Ubangijin iyayenku magabata".**
**(27) Sai Fir'auna ya ce: "Lallai wannan wanda yake riyawa cewa shi Manzo ne da ako turo muku mahaukaci ne, bai san yadda zai bayar da amsa ba, yana faxin abin da hankali ba zai xauka ba".**
**(28) Sai Annabi Musa ya ce: "Allan da nake kiranku zuwa gare shi, shi ne, Ubangijin gabas da yamma da abin da ke tsakaninsu, in kuna da hankalin da zaku hankalta da shi".**
**(29) Sai Fir'auna yace wa Annabi Musa, bayan ya gajiya wajen muhawara da shi: "Lallai in ka bautawa wani abin bauta, ba ni ba, to lallai sai na saka ka cikin gidan kurkuku".**
**(30) Sai Annabi Musa (A.S) ya cewa Fir'auna: "Zaka saka ni cikin gidan kurkuku, koda na zo maka da abin da zai bayyana gaskiyar abin da na zo maka da shi daga wurin Allah?".**
**(31) Sai Fir'auna ya ce: "To, ka zo da abin da ka faxa, cewa zai nuna gaskiyarka xin, in har ka kasance cikin masu gaskiya a abin da kake da'awarsa".**
**(32) Sai Annabi Musa (A.S) ya jefa sandarsa a qasa, sai ta riqixe ta zama macijiya bayyananniya, kowa yana ganinta.**
**(33) Kuma ya shigar da hannunsa a wuyan rigarsa, ba wani fari tare da shi, amma sai ya fitar da shi fari, fari mai haske, ba na cuta ba, masu kallo suna ganinsa a hakan.**
**(34) Sai Fir'auna ya cewa manyan mutanensa da suke gefensa: "Lallai wannan mutumin matsafi ne, gwanin iya tsafi". (35) "Yana son ya fitar da ku ne daga garinku da tsafinsa, me nene ra'ayinku dangane da matakin da zamu xauka a kansa?"**
**(36) Sai suka ce masa: "Ka dakatar da shi, da xan 'uwansa, kar ka yi gaggawar yi musu uquba. Ka tura waxanda zasu taro matsafa daga biranen Misra".**
**(37) Su taho maka da duk wani matsafi, gwani cikin sanin tsafi".**
**(38) Sai Fir'auna ya tara matsafansa, domin yin 'yar qure da Annabi Musa, a wani wuri, da lokaci ayyanannu.**
**(39) Ka cewa mutane: "Ko zaku taru don ku ga waye zai yi galaba, Musa ne ko matsafa?".**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Kurakuran mai da'awa da suka gabata, da ni'imomin da aka yi masa, basa hana shi ya yi kira ga wanda ya yi musu kuskuren, ko ga waxanda suka yi masa ni'imar. 2 - Riqo da sababi na kariya daga abokin gaba, baya kore imani da dogaro ga Allah. 3 - Halittun Allah suna nuna Ubangijintakarsa da kaxaitakarsa. 4 - Raunin hujja xaya ne daga cikin sabubban da suke sa a yi tashin hankali. 5 - Tunzura gama-garin mutane a kan masu addini, tafarki ne na fanxararrun shugabanni.**

لَعَلَّنَا نَتَّبِعُ ٱلسَّحَرَةَ إِن كَانُواْ هُمُ ٱلْغَٰلِبِينَ ٤٠ فَلَمَّا جَآءَ ٱلسَّحَرَةُ
قَالُواْ لِفِرْعَوْنَ أَئِنَّ لَنَا لَأَجْرًا إِن كُنَّا نَحْنُ ٱلْغَٰلِبِينَ ٤١ قَالَ نَعَمْ
وَإِنَّكُمْ إِذًا لَّمِنَ ٱلْمُقَرَّبِينَ ٤٢ قَالَ لَهُم مُّوسَىٰٓ أَلْقُواْ مَآ أَنتُم مُّلْقُونَ
٤٣ فَأَلْقَوْاْ حِبَالَهُمْ وَعِصِيَّهُمْ وَقَالُواْ بِعِزَّةِ فِرْعَوْنَ إِنَّا لَنَحْنُ
ٱلْغَٰلِبُونَ ٤٤ فَأَلْقَىٰ مُوسَىٰ عَصَاهُ فَإِذَا هِىَ تَلْقَفُ مَا يَأْفِكُونَ
٤٥ فَأُلْقِىَ ٱلسَّحَرَةُ سَٰجِدِينَ ٤٦ قَالُوٓاْ ءَامَنَّا بِرَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ٤٧
رَبِّ مُوسَىٰ وَهَٰرُونَ ٤٨ قَالَ ءَامَنتُمْ لَهُۥ قَبْلَ أَنْ ءَاذَنَ لَكُمْ إِنَّهُۥ
لَكَبِيرُكُمُ ٱلَّذِى عَلَّمَكُمُ ٱلسِّحْرَ فَلَسَوْفَ تَعْلَمُونَ لَأُقَطِّعَنَّ أَيْدِيَكُمْ
وَأَرْجُلَكُم مِّنْ خِلَٰفٍ وَلَأُصَلِّبَنَّكُمْ أَجْمَعِينَ ٤٩ قَالُواْ لَا ضَيْرَ إِنَّآ
إِلَىٰ رَبِّنَا مُنقَلِبُونَ ٥٠ إِنَّا نَطْمَعُ أَن يَغْفِرَ لَنَا رَبُّنَا خَطَٰيَٰنَآ أَن كُنَّآ
أَوَّلَ ٱلْمُؤْمِنِينَ ٥١ ۞ وَأَوْحَيْنَآ إِلَىٰ مُوسَىٰٓ أَنْ أَسْرِ بِعِبَادِىٓ إِنَّكُم ثلاثة أرباع الحزب ٣٧
مُّتَّبَعُونَ ٥٢ فَأَرْسَلَ فِرْعَوْنُ فِى ٱلْمَدَآئِنِ حَٰشِرِينَ ٥٣ إِنَّ هَٰٓؤُلَآءِ
لَشِرْذِمَةٌ قَلِيلُونَ ٥٤ وَإِنَّهُمْ لَنَا لَغَآئِظُونَ ٥٥ وَإِنَّا لَجَمِيعٌ حَٰذِرُونَ
٥٦ فَأَخْرَجْنَٰهُم مِّن جَنَّٰتٍ وَعُيُونٍ ٥٧ وَكُنُوزٍ وَمَقَامٍ كَرِيمٍ ٥٨
كَذَٰلِكَ وَأَوْرَثْنَٰهَا بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ ٥٩ فَأَتْبَعُوهُم مُّشْرِقِينَ ٦٠



**40 da fatan zamu bi masu sihiri cikin addininsu in ya kasance sun yi galaba a kan Musa.**
**41 Yayin da masu sihiri suka zo wurin Fir'auna don su qure Annabi Musa, sai suka ce masa: "Shin muna da wani lada, wanda ake gani, ko wanda ba a gani, idan mun yi galaba a kan Musa?".**
**42 Sai Fir'auna yace musu: "Na'am, kuna da lada. don in kun yi galaba a kansa zaku zama cikin makusantana, ta hanyar baku manya-manyan muqamai". 43 Sai Annabi Musa ya ce musu, yana mai tabbacin samun taimakon Allah, kuma yana mai bayyana musu cewa abin da yake tare da shi ba tsafi ba ne,: "Ku jefa duk abin da zaku iya jefawa na igiyoyinku da sandunanku".**
**44 Sai suka jefa igiyoyinsu da sandunansu, kuma suka ce, a yayin da suke jefa su: "Da girman Fir'auna, mu ne masu galaba, kuma Musa shi ne za a yi galaba a kansa". 45 Sai Annabi Musa ya jefa sandarsa sai ta riqixe ta zama macijiya, kwatsam sai ga ta tana haxiye abin da suke yaudarar mutane da shi na tsafi. 46 Yayin da matsafa suka ga sandar Annabi Musa tana haxiye abin da suka jefa na tsafinsu, sai suka faxi suna masu sujjada. 47 Suka ce: "Mun yi imani da Ubangijin talikai baki xaya".**
**48 Ubangijin Annabi Musa da Haruna (A.S).**
**49 Sai Fir'auna ya ce, yana mai inkari ga waxannan matsafa bisa imaninsu: "Yanzu kun yi imani da Musa tun kafin na yi muku izinin yin hakan?! Lallai Musa shi ne babbanku wanda ya koya muku tsafi. Kuma kun haxa baki ne gaba xayanku don ku fitar da mutanen Misra daga cikinta, to sannu zaku ga abin da zan muku na uquba. Tabbas sai na yanke hannuwa da qafafun ku a rarrabe, hanun dama da qafar hagu, da hannun hagu da qafar dama, kuma tabbas sai na tsire ku akan kututturen itacen Dabino, ba zan qyale ko xaya daga cikin ku ba". 50 Sai Matsafan suka cewa Fir'auna: "Babu wata cutuwa cikin abin da kake mana gargaxinsa, na yayyankawa da tsirewa a duniya, saboda azabarka zata gushe, kuma zamu koma zuwa ga Ubangijinmu, kuma zai shigar da mu cikin rahamarsa dauwamammiya.**
**51 Haqiqa muna fatan Allah ya shafe mana zunuban mu da muka aikata, waxanda suka gabata, saboda mun kasance farkon waxanda suka yi imani da Annabi Musa, suka gasgata shi.**
**52 Mun yi wahayi ga Annabi Musa, Muna masu umartar sa da cewa ya tafi da bani Isra'ila da daddare, kuma Fir'auna da mabiyansa zasu biyo bayansu don su mayar da su". 53 Sai Fir'auna ya aika wasu daga cikin rundunarsa zuwa ga garuruwan Misra, su tara masa rundunoni, domin su dawo da Bani Isra'ila, yayin da ya san labarin fitarsu daga garin Misra.**
**54 Fir'auna ya ce, yana mai rena sha'anin Bani Isra'ila: "Haqiqa waxannan wasu 'yan jama'a ne 'yan kaxan".**
**55 "Kuma suna aikata abin da ya saka muke ji haushinsu".**
**56 Kuma lallai mu a shirye muke, mun san me suke aikatawa".**
**57 Sai Muka fitar da Fir'auna da mutanensa daga garin Misra, gari kyawawan lambuna kore shar, da idanuwan ruwa masu gudana. 58 Da taskokin dukiya da kyawawan gidaje. 59 Kamar yadda muka fitar da Fir'auna da mutanensa daga waxannan ni'imomin, to irin waxannan ni'imomi ne muka ba wa bani Isra'ila a garuruwan Sham.**
**60 Sai Fir'auna da mutanensa suka biyo bayan Bani Isra'ila a daidai lokacin vullowar hasken rana.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Alaqar dake tsakanin mavarnata da junansu ita ce alaqar neman duniya kawai. 2 - Tabbacin Annabi Musa na samun nasara akan matsafa, saboda gasgata alqawarin da Allah ya yi masa. 3 - Imanin da matsafa suka yi dalili ne da yake nuna zukatan bayi a hannun Allah suke, yana jujjuya su yadda ya ga dama. 4 - Shisshigi da zalunci suna daga cikin sabubban da suke sa mulki ya gushe.**

فَلَمَّا تَرَٰٓءَا ٱلۡجَمۡعَانِ قَالَ أَصۡحَٰبُ مُوسَىٰٓ إِنَّا لَمُدۡرَكُونَ ٦١
قَالَ كَلَّآۖ إِنَّ مَعِيَ رَبِّي سَيَهۡدِينِ ٦٢ فَأَوۡحَيۡنَآ إِلَىٰ مُوسَىٰٓ أَنِ
ٱضۡرِب بِّعَصَاكَ ٱلۡبَحۡرَۖ فَٱنفَلَقَ فَكَانَ كُلُّ فِرۡقٖ كَٱلطَّوۡدِ ٱلۡعَظِيمِ
٦٣ وَأَزۡلَفۡنَا ثَمَّ ٱلۡأٓخَرِينَ ٦٤ وَأَنجَيۡنَا مُوسَىٰ وَمَن مَّعَهُۥٓ أَجۡمَعِينَ
٦٥ ثُمَّ أَغۡرَقۡنَا ٱلۡأٓخَرِينَ ٦٦ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَةٗۖ وَمَا كَانَ
أَكۡثَرُهُم مُّؤۡمِنِينَ ٦٧ وَإِنَّ رَبَّكَ لَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلرَّحِيمُ ٦٨
وَٱتۡلُ عَلَيۡهِمۡ نَبَأَ إِبۡرَٰهِيمَ ٦٩ إِذۡ قَالَ لِأَبِيهِ وَقَوۡمِهِۦ مَا تَعۡبُدُونَ
٧٠ قَالُواْ نَعۡبُدُ أَصۡنَامٗا فَنَظَلُّ لَهَا عَٰكِفِينَ ٧١ قَالَ هَلۡ
يَسۡمَعُونَكُمۡ إِذۡ تَدۡعُونَ ٧٢ أَوۡ يَنفَعُونَكُمۡ أَوۡ يَضُرُّونَ ٧٣ قَالُواْ
بَلۡ وَجَدۡنَآ ءَابَآءَنَا كَذَٰلِكَ يَفۡعَلُونَ ٧٤ قَالَ أَفَرَءَيۡتُم مَّا كُنتُمۡ
تَعۡبُدُونَ ٧٥ أَنتُمۡ وَءَابَآؤُكُمُ ٱلۡأَقۡدَمُونَ ٧٦ فَإِنَّهُمۡ عَدُوّٞ لِّيٓ
إِلَّا رَبَّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٧٧ ٱلَّذِي خَلَقَنِي فَهُوَ يَهۡدِينِ ٧٨ وَٱلَّذِي هُوَ
يُطۡعِمُنِي وَيَسۡقِينِ ٧٩ وَإِذَا مَرِضۡتُ فَهُوَ يَشۡفِينِ ٨٠ وَٱلَّذِي
يُمِيتُنِي ثُمَّ يُحۡيِينِ ٨١ وَٱلَّذِيٓ أَطۡمَعُ أَن يَغۡفِرَ لِي خَطِيٓـَٔتِي
يَوۡمَ ٱلدِّينِ ٨٢ رَبِّ هَبۡ لِي حُكۡمٗا وَأَلۡحِقۡنِي بِٱلصَّٰلِحِينَ ٨٣



**(61) Yayin da Fir'auna da mutanensa suka fuskanci Annabi Musa da mutanensa, ta yadda kowane vangare ya yi ido huxu da xaya vangaren, sai mutanen Annabi Musa suka ce: "Haqiqa Fir'auna da mutanensa zasu kamo mu, kuma ba zamu iya da su ba". (62) Sai Annabi Musa ya cewa mutanensa: "Abin ba kamar yadda kuke surantawa ba ne. Tabbas Ubangijina yana tare da ni da kariyarsa da qarfafawarsa, zai shiryar da ni kuma ya nuna mini hanyar tsira". (63) Sai muka yi wa Annabi Musa wahayi, muna masu umurtar sa da ya bugi teku da sandarsa. Sai ya buge shi da ita. Sai tekun ya rabe biyu, ya zama hanyoyi goma sha biyu, adadin qabilun Bani Isra'ila, kowane vangare na tekun da ya tsage sai ya zama kamar qaton dutse wajen girma da tabbatuwa, ta yadda ruwa baya gudana a cikinsa. (64) Muka kusanto da Fir'auna da mutanensa, har suka shiga cikin tekun, suna zaton cewa hanyar mai vullewa ce.**

**(65) Sai muka tseratar da Annabi Musa da waxanda suke tare da shi, daga cikin Bani Isra'il, babu wanda ya halaka daga cikinsu.**

**(66) Sannan muka halakar da Fir'auna da mutanensa, ta hanyar nutsar da su a cikin tekun.**

**(67) Haqiqa a cikin rabuwar tekun gida biyu, ga Annabi Musa, da quvutar da shi da mutanensa, da kuma halakar da Fir'auna da mutanensa, akwai dalili da yake nuna gaskiyar Annabi Musa. Amma mafiya yawan waxanda suke tare da Fir'auna basu kasance masu imani ba.**

**(68) Kuma lallai Ubangijinka – Ya kai wannan Manzo- shi ne Mabuwayi, wanda yake xaukan fansa a kan abokan gabarsa, kuma mai jin qai ga wanda ya tuba a cikinsu.**

**(69) Kuma - Ya kai wannan Manzo- ka karanta musu qissar Annabi Ibrahim.**

**(70) Yayin da ya ce wa babansa Azara da mutanensa: "Mene ne wannan da kuke bautawa koma bayan Allah?".**

**(71) Sai Mutanensa suka ce: "Muna bautar gumaka ne, waxanda muke tabbata a kan bauta musu, muna masu lazimtar hakan". (72) Sai Annabi Ibrahim ya ce musu: "Shin gumakan suna jin addua'rku yayin da kuke kiransu?".**

**(73) "Ko suna amfanarku in kun yi musu biyayya, ko su cutar da ku in kun sava musu?".**

**(74) Suka ce: "Ba sa jin mu idan mun kira su, basa amfanar da mu idan mun yi musu biyayya, kuma basa cutar da mu idan mun sava musu, kawai dai mun samu iyayenmu suna yin haka ne, don haka muke koyi da su".**

**(75) Sai Annabi Ibrahim ya ce da su: "Ku lura, kun ga abin da kuke bautawa na gumaka koma bayan Allah?"**

**(76) Da abin da iyayenku na farko suke bautawa?"**

**(77) To dukkaninsu abokan gaba ta ne, saboda dukkaninsu qarya ne, sai dai Allah Ubangijin talikai baki xaya".**

**(78) "Wanda ya halicce ni, kuma shi ne yake shiryar da ni zuwa ga alheran duniya da lahira".**

**(79) "Kuma wanda shi ne kaxai yake ciyar da ni idan na ji yunwa, kuma yake shayar da ni idan na ji qishirwa".**

**(80) "Kuma idan na yi rashin lafiya, shi ne kaxai yake warkar mini da cuta, babu mai warkar da ni koma bayan shi".**

**(81) "Kuma wanda shi ne, shi kaxai zai karvi raina idan ajalina ya cika, kuma ya raya ni bayan mutuwa ta".**

**(82) "Kuma wanda shi kaxai nake fatan ya gafarta mini kurakurai na a ranar sakamako".**

**(83) Annabi Ibrahim ya ce, yana mai roqon Ubangijinsa: "Ya Ubangijina, ka ba ni fahimta cikin addini, kuma ka haxa ni da nagartattun bayi, daga cikin Annabawan da suka gabace ne, ka shigar da ni Aljanna tare da su".**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Allah yana tare da bayinsa Muminai, ta hanyar basu nasara da qarfafawa, da tseratar wa daga tsanani. 2 - Tabbatar da siffar buwaya (Izza) da jin qai (Rahama) ga Allah Maxaukakin Sarki. 3 - Haxarin makauniyar biyayya.**
**4 - Fatan da mumini yake da shi a wurin Ubangijinsa mai girma ne.**

وَٱجۡعَل لِّي لِسَانَ صِدۡقٖ فِي ٱلۡأٓخِرِينَ ٨٤ وَٱجۡعَلۡنِي مِن وَرَثَةِ جَنَّةِ
ٱلنَّعِيمِ ٨٥ وَٱغۡفِرۡ لِأَبِيٓ إِنَّهُۥ كَانَ مِنَ ٱلضَّآلِّينَ ٨٦ وَلَا تُخۡزِنِي يَوۡمَ
يُبۡعَثُونَ ٨٧ يَوۡمَ لَا يَنفَعُ مَالٞ وَلَا بَنُونَ ٨٨ إِلَّا مَنۡ أَتَى ٱللَّهَ بِقَلۡبٖ
سَلِيمٖ ٨٩ وَأُزۡلِفَتِ ٱلۡجَنَّةُ لِلۡمُتَّقِينَ ٩٠ وَبُرِّزَتِ ٱلۡجَحِيمُ لِلۡغَاوِينَ
٩١ وَقِيلَ لَهُمۡ أَيۡنَ مَا كُنتُمۡ تَعۡبُدُونَ ٩٢ مِن دُونِ ٱللَّهِ هَلۡ يَنصُرُونَكُمۡ
أَوۡ يَنتَصِرُونَ ٩٣ فَكُبۡكِبُواْ فِيهَا هُمۡ وَٱلۡغَاوُۥنَ ٩٤ وَجُنُودُ إِبۡلِيسَ
أَجۡمَعُونَ ٩٥ قَالُواْ وَهُمۡ فِيهَا يَخۡتَصِمُونَ ٩٦ تَٱللَّهِ إِن كُنَّا لَفِي
ضَلَٰلٖ مُّبِينٍ ٩٧ إِذۡ نُسَوِّيكُم بِرَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ٩٨ وَمَآ أَضَلَّنَآ إِلَّا
ٱلۡمُجۡرِمُونَ ٩٩ فَمَا لَنَا مِن شَٰفِعِينَ ١٠٠ وَلَا صَدِيقٍ حَمِيمٖ ١٠١ فَلَوۡ
أَنَّ لَنَا كَرَّةٗ فَنَكُونَ مِنَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ١٠٢ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَةٗۖ وَمَا كَانَ
أَكۡثَرُهُم مُّؤۡمِنِينَ ١٠٣ وَإِنَّ رَبَّكَ لَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلرَّحِيمُ ١٠٤ كَذَّبَتۡ
قَوۡمُ نُوحٍ ٱلۡمُرۡسَلِينَ ١٠٥ إِذۡ قَالَ لَهُمۡ أَخُوهُمۡ نُوحٌ أَلَا تَتَّقُونَ ١٠٦
إِنِّي لَكُمۡ رَسُولٌ أَمِينٞ ١٠٧ فَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُونِ ١٠٨ وَمَآ أَسۡـَٔلُكُمۡ
عَلَيۡهِ مِنۡ أَجۡرٍۖ إِنۡ أَجۡرِيَ إِلَّا عَلَىٰ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ١٠٩ فَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ
وَأَطِيعُونِ ١١٠ ۞ قَالُوٓاْ أَنُؤۡمِنُ لَكَ وَٱتَّبَعَكَ ٱلۡأَرۡذَلُونَ ١١١

الحزب ٣٨



**(84) Kuma ka sanya mini kyakkyawan ambato da
kyakkyawan yabo cikin waxanda zasu zo bayana
daga qarnoni masu zuwa. (85) Kuma ka sanya
ni cikin wanxanda za su gaji gidajen Aljannah,
waxanda bayinka muminai suke jin daxi a
cikinsu, ka zaunar da ni a cikinsu. (86) Kuma ka
gafarta wa babana, haqiqa shi ya kasance cikin
waxanda suka vace daga tafarkin gaskiya, saboda
shirka. Annabi Ibrahim ya yi wa babansa addu'a
ne, kafin ya bayyana gare shi cewa xan wuta ne.
Yayin da ya bayyana gare shi, sai ya barranta
daga gare shi, bai sake yi mi shi addu'a ba.
(87) “Kuma kada ka kunyata ni da azaba, a ranar
da za a tayar da mutane don a yi musu hisabi”.
(88) Ranar da dukiyar da mutum ya tara a
duniyarsa ba zata yi masa amfani ba, haka nan
'yayan da yake ba su kariya”. (89) Sai dai wanda
ya zo wa Allah da kuvutacciyar zuciya, wadda
babu shirka, babu munafinci, babu riya, babu ji-
ji-da-kai a cikinta, to shi zai amfana da dukiyarsa
wadda ya ciyar da ita don xaukaka kalmar Allah,
kuma zai amfana da 'ya'yansa waxanda suke masa
addu'a. (90) Kuma za a kusanto da Aljanna zuwa
ga masu jin tsoron, Allah, ta hanyar kamanta
umarninsa da nesantar haninsa. (91) Kuma aka
fito da wuta a farfajiyar taron alqiyama, ga
vatattu waxanda suka vace daga addinin gaskiya.
(92) Kuma za a ce musu, don tsawatarwa a gare
su: “Ina abin da kuka kasance kuna bautawa na
gumaka?”. (93) “Waxanda kuke bauta musu koma
bayan Allah? Shin za su agaza muku, su kare ku
daga azabar Allah, ko za su agaza wa kawunansu?”
(94) Sai jefa su a cikin wutan Jaheem, sahensu a
kan sashe, su da waxanda suka vatar da su.
(95) Da mataimakan shaixan gaba xayansu, ba za
a toge kowa daga cikinsu ba. (96) Mushirikai waxanda suka kasance suna bautar wanin Allah, suna xaukansu a
matsayin kishiyoyi ga Allah, za su ce, a yayin da suke husuma da waxanda suka kasance suna bautawa koma bayan
Allah. (97) “Wallahi lallai mun kasance cikin vata mabayyani daga tafarkin gaskiya”. (98) Yayin da muke daidaita
ku da Ubangijin talikai baki xaya, muna bauta muku, kamar yadda muke bauta masa. (99) Babu wanda ya vatar
da mu daga tafarkin gaskiya sai masu laifi, waxanda suka kira mu zuwa ga bauta musu koma bayan Allah”. (100) Ga
shi bamu da masu ceto da zasu cece mu a wurin Allah, don ya kuvutar da mu daga azabarsa. (101) Kuma bamu da
wani aboki, mai tsantsan soyayya, wanda zai kare mu, ya cece mu. (102) Da za a mayar da mu rayuwar duniya, da sai
mu kasance cikin masu imani da Allah. (103) Lallai a cikin wannan abin da aka ambata daga qissar Annabi Ibrahim
(A.S), da makomar masu qaryata Manzanni, akwai abin la'akari ga masu xaukar izina, amma mafi yawansu ba su
kasance masu imani ba. (104) Kuma lallai Ubangijinka – Ya kai wannan Manzo- Mabuwayi ne, wanda yake xaukar
fansa a kan abokan gabarsa, mai jin qai ga wanda ya tuba daga cikinsu. (105) Mutanen Annabi Nuhu sun qaryata
Manzanni, yayin da suka qaryata Annabi Nuhu (A.S). (106) Yayin da Annabi Nuhu (A.S) ya ce musu: “Me yasa ba
zaku ji tsoron Allah ba, ku bar bautar wani ba shi ba don jin tsoronsa?!”. (107) “Lallai ni Manzo ne zuwa gare ku,
wanda Allh ya aiko ni, zuwa wurinku, mai amana, ba zan qara komai akan abin da Allah ya yi min wahayinsa ba,
kuma ba zan rage komai ba”. (108) Don haka ku ji tsoron Allah ta hanyar kamanta umarninsa, da nesantar haninsa,
kuma ku yi min biyayya cikin abin da nake yi muku umarni da shi, da abin da nake muku hani a kai”. (109) “Kuma
bana neman wani lada a wurinku na abin da nake isar muku daga Ubangijina, ladana ba ya wajen kowa sai Allah,
Ubangijin talikai baki xaya, ban da waninsa”. (110) “Don haka ku ji tsoron Allah ta hanyar kamanta umarninsa, da
nesantar haninsa, kuma ku yi min biyayya cikin abin da na yi muku umarni da shi da, abin da nake muku hani a
kai”. (111) Sai mutanensa suka ce masa: “Yanzu zamu yi imani da kai – Ya kai Nuhu- mu bi abin da ka zo da shi, mu
yi aiki da shi, alhali mabiyanka su ne qasqantattu a cikin mutane, babu wasu manya da shugabanni a cikinsu?!”.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Muhimmancin kuvutar zuciya daga cututtuka, irinsu hassada da riya da ji-ji-da-kai. 2 - Jingina haqqin vacewa a kan waxanda suka vatar da mutum ba zai amfani vatattu ba. 3 - Qaryata Manzon Allah guda xaya, qaryata dukkan Manzanni ne gaba xayansu. 4 - Kyakkyawan tsarin zance a cikin wannan qissa ta Annabi Ibrahim, ta yadda aka shiga bayanin tashin alqiyama, sannan kuma aka dawo zuwa ga qarshen qissar.**

قَالَ وَمَا عِلۡمِي بِمَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ١١٢ إِنۡ حِسَابُهُمۡ إِلَّا عَلَىٰ رَبِّيۖ
لَوۡ تَشۡعُرُونَ ١١٣ وَمَآ أَنَا۠ بِطَارِدِ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ١١٤ إِنۡ أَنَا۠ إِلَّا نَذِيرٞ مُّبِينٞ
١١٥ قَالُواْ لَئِن لَّمۡ تَنتَهِ يَٰنُوحُ لَتَكُونَنَّ مِنَ ٱلۡمَرۡجُومِينَ ١١٦ قَالَ
رَبِّ إِنَّ قَوۡمِي كَذَّبُونِ ١١٧ فَٱفۡتَحۡ بَيۡنِي وَبَيۡنَهُمۡ فَتۡحٗا وَنَجِّنِي وَمَن
مَّعِيَ مِنَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ١١٨ فَأَنجَيۡنَٰهُ وَمَن مَّعَهُۥ فِي ٱلۡفُلۡكِ ٱلۡمَشۡحُونِ
١١٩ ثُمَّ أَغۡرَقۡنَا بَعۡدُ ٱلۡبَاقِينَ ١٢٠ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَةٗۖ وَمَا كَانَ
أَكۡثَرُهُم مُّؤۡمِنِينَ ١٢١ وَإِنَّ رَبَّكَ لَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلرَّحِيمُ ١٢٢ كَذَّبَتۡ
عَادٌ ٱلۡمُرۡسَلِينَ ١٢٣ إِذۡ قَالَ لَهُمۡ أَخُوهُمۡ هُودٌ أَلَا تَتَّقُونَ ١٢٤ إِنِّي لَكُمۡ
رَسُولٌ أَمِينٞ ١٢٥ فَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُونِ ١٢٦ وَمَآ أَسۡـَٔلُكُمۡ عَلَيۡهِ
مِنۡ أَجۡرٍۖ إِنۡ أَجۡرِيَ إِلَّا عَلَىٰ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ١٢٧ أَتَبۡنُونَ بِكُلِّ رِيعٍ
ءَايَةٗ تَعۡبَثُونَ ١٢٨ وَتَتَّخِذُونَ مَصَانِعَ لَعَلَّكُمۡ تَخۡلُدُونَ ١٢٩
وَإِذَا بَطَشۡتُم بَطَشۡتُمۡ جَبَّارِينَ ١٣٠ فَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُونِ ١٣١
وَٱتَّقُواْ ٱلَّذِيٓ أَمَدَّكُم بِمَا تَعۡلَمُونَ ١٣٢ أَمَدَّكُم بِأَنۡعَٰمٖ وَبَنِينَ
١٣٣ وَجَنَّٰتٖ وَعُيُونٍ ١٣٤ إِنِّيٓ أَخَافُ عَلَيۡكُمۡ عَذَابَ يَوۡمٍ عَظِيمٖ
١٣٥ قَالُواْ سَوَآءٌ عَلَيۡنَآ أَوَعَظۡتَ أَمۡ لَمۡ تَكُن مِّنَ ٱلۡوَٰعِظِينَ ١٣٦



(112) Sai Annabi Nuhu (A.S) yace musu: "Me ya sanar da ni abin da waxannan muminai suke aikatawa? Ai ni ba mai gaidin su ba ne, wanda zan qididdige ayyukansu". (113) Hisabin su baya kan kowa, sai a wurin Allah, wanda ya san abin da suke voyewa da wanda suka bayyana, ba ni ne zan yi musu ba, da kuna da sani da baku faxi abin da kuka faxa ba". (114) Kuma ni ba zan kori Muminai daga majalisa ta ba, in muku abin da kuka nema, don ku ku yi imani. (115) Ni ba kowa ba ne face mai yin gargaxi a bayyane, ina muku kashedi da azabar Allah. (116) Mutanensa suka ce masa: "Lallai in baka daina kiranmu zuwa ga abin da kake kira ba, to tabbas za ka kasance abin zagi da kisa ta hanyar jifa da duwatsu". (117) Annabi Nuhu (A.S) ya ce, yana mai roqon Ubangijinsa: "Ya Ubangijina, haqiqa mutane na sun qaryata ni, ba su gasgata ni cikin abin da na zo musu da shi daga wurinka ba". (118) Don haka ka yi hukunci tsakanina da su, hukuncin da zai halaka su, saboda dogewarsu a kan qarya, kuma ka tserar da ni da da waxanda suke tare da ni cikin Muminai daga abin da zaka halaka kafirai da shi cikin mutane na. (119) Sai muka amsa masa addu'arsa, muka tserar da shi da waxanda suke tare da shi daga cikin Muminai, a jirgin ruwa, wanda yake cike da mutane da dabbobi. (120) Sannan kuma sai muka halakar da sauran, wato mutanen Annabi Nuhu. (121) Lallai a cikin wannan abin da aka ambata na qissar Annabi Nuhu da mutanensa, da kuvutar da Annabi Nuhu da wanxanda suke tare da shi daga Muminai, da halakar da kafirai daga cikin mutanensa, akwai izina ga masu la'akari, amma mafi yawansu basu kasance masu imani ba.
(122) Haqiqa Ubangijinka – Ya kai wannan Manzo- Mabuwayi ne, wanda yake xaukan fansa a kan abokan gabarsa, kuma mai jin qai ga wanda ya tuba daga cikinsu. (123) Adawa sun qaryata Manzanni, yayin da suka qaryata Manzonsu Annabi Hudu (A.S). (124) Ka tuna lokacin da Annabinsu, Annabi Hudu ya ce da su: "Ba za ku ji tsoron Allah ba, ku daina bauta wa waninsa, saboda kawai kuna jin tsoronsa?!". (125) "Haqiqa ni Manzonku ne, wanda Allah ya aiko ni zuwa wurinku, kuma amintacce, ba zan qara komai cikin abin da Allah ya yi min umarnin in isar da shi ba, kuma ba zan rage komai ba". (126) Don haka ku ji tsoron Allah ta hanyar kamanta umarninsa da nesantar haninsa, kuma ku yi min biyayya cikin abin da na yi muku umarni da shi, da abin da na hana ku". (127) Kuma ba na neman wani lada a wurinku, na abin da nake isar muku daga Ubangijina, ladana baya wajen kowa sai Allah, Ubangijin talikai baki xaya, ba a wajen waninsa ba. (128) Yanzu zaku rinqa gina gidajen a kowane tudu da wuri mai girma, ba tare da wata fa'ida, da zaku samu a duniya da lahira?!". (129) Kuna gina manya manyan gine-gine da benaye, kamar zaku dawwama a wannan duniya, ba zaku bar ta ba?!
(130) Kuma idan kuka dira da kisa ko duka, sai ku dira cikin girman kai, babu rangwame ko tausayi.
(131) To ku ji tsoron Allah, ta hanyar kamanta umarninsa, da nesantar haninsa, kuma ku yi mini biyayya cikin abin da na yi muku umarni da shi, da abin da nake muku hani a kai. (132) Kuma ku ji tsoron fushin Allah, wanda ya ba ku ni'imominsa waxanda kuka sani. (133) Ya ba ku dabbobi, ya ba ku 'ya'ya. (134) ya ba ku gonaki da idanuwan ruwa masu gudana. (135) Haqiqa – Ya ku mutane na – ina ji muku tsoron azabar wata rana mai girma, ita ce ranar alqiyama. (136) Sai mutanensa suka ce masa: "Tunatarwar ka a gare mu da ranshinta duk xaya nea wurin mu. Ba zamu tava yin imani da kai ba, ba zamu dawo daga kan abin da muke a kai ba.

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** 1 - Falalar waxanda suka riga yin imani koda kuwa sun kasance talakawa ne ko masu rauni. 2 - Halakar da azzalumai da tserar da Muminai sunna ce ta Allah. 3 - Haxarin karkata zuwa ga duniya. 4 - Taurin kan masu varna da dogewarsu a kanta.

إِنۡ هَٰذَآ إِلَّا خُلُقُ ٱلۡأَوَّلِينَ ١٣٧ وَمَا نَحۡنُ بِمُعَذَّبِينَ ١٣٨ فَكَذَّبُوهُ
فَأَهۡلَكۡنَٰهُمۡۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَةٗۖ وَمَا كَانَ أَكۡثَرُهُم مُّؤۡمِنِينَ ١٣٩
وَإِنَّ رَبَّكَ لَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلرَّحِيمُ ١٤٠ كَذَّبَتۡ ثَمُودُ ٱلۡمُرۡسَلِينَ ١٤١ إِذۡ
قَالَ لَهُمۡ أَخُوهُمۡ صَٰلِحٌ أَلَا تَتَّقُونَ ١٤٢ إِنِّي لَكُمۡ رَسُولٌ أَمِينٞ ١٤٣
فَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُونِ ١٤٤ وَمَآ أَسۡـَٔلُكُمۡ عَلَيۡهِ مِنۡ أَجۡرٍۖ إِنۡ أَجۡرِيَ
إِلَّا عَلَىٰ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ١٤٥ أَتُتۡرَكُونَ فِي مَا هَٰهُنَآ ءَامِنِينَ ١٤٦
فِي جَنَّٰتٖ وَعُيُونٖ ١٤٧ وَزُرُوعٖ وَنَخۡلٖ طَلۡعُهَا هَضِيمٞ ١٤٨
وَتَنۡحِتُونَ مِنَ ٱلۡجِبَالِ بُيُوتٗا فَٰرِهِينَ ١٤٩ فَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُونِ
١٥٠ وَلَا تُطِيعُوٓاْ أَمۡرَ ٱلۡمُسۡرِفِينَ ١٥١ ٱلَّذِينَ يُفۡسِدُونَ فِي ٱلۡأَرۡضِ
وَلَا يُصۡلِحُونَ ١٥٢ قَالُوٓاْ إِنَّمَآ أَنتَ مِنَ ٱلۡمُسَحَّرِينَ ١٥٣ مَآ أَنتَ
إِلَّا بَشَرٞ مِّثۡلُنَا فَأۡتِ بِـَٔايَةٍ إِن كُنتَ مِنَ ٱلصَّٰدِقِينَ ١٥٤ قَالَ
هَٰذِهِۦ نَاقَةٞ لَّهَا شِرۡبٞ وَلَكُمۡ شِرۡبُ يَوۡمٖ مَّعۡلُومٖ ١٥٥ وَلَا تَمَسُّوهَا
بِسُوٓءٖ فَيَأۡخُذَكُمۡ عَذَابُ يَوۡمٍ عَظِيمٖ ١٥٦ فَعَقَرُوهَا فَأَصۡبَحُواْ
نَٰدِمِينَ ١٥٧ فَأَخَذَهُمُ ٱلۡعَذَابُۚ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَةٗۖ وَمَا كَانَ
أَكۡثَرُهُم مُّؤۡمِنِينَ ١٥٨ وَإِنَّ رَبَّكَ لَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلرَّحِيمُ ١٥٩



**(137) Wannan ba komai ba ne face addinin mutanen
farko da al'adunsu da xabi'unsu. (138) Kuma ba
za a yi mana azaba. (139) Sai suka zarce a kan
qaryata Annabinsu, Annabi Hudu (A.S), sai
muka halaka su a sakamakon qaryatawarsu
da iska bakararriya. Lallai a cikin wannan
halakarwar akwai abin izina ga masu la'akari,
amma mafi yawansu basu kasance masu imani
ba. (140) Kuma lallai Ubangijinka – Ya kai wannan
Manzo- Mabuwayi ne, wanda yake xaukan fansa
a kan abokan gabarsa, kuma mai jin qai ne ga
wanda ya tuba a cikinsu. (141) Samudawa sun
qaryata Manzanni, da suka qaryata Manzonsu
Annabi Salihu (A.S). (142) Yayin da xa'uwansu na
dangantaka Annabi Salihu ya ce musu: "Shin ba
zaku ji tsoron Allah ba, ku bar bautar waninsa
don kuna jin tsoronsa?!". (143) "Haqiqa ni Manzon
ne gare ku, wanda Allah ya aiko ni zuwa wurinku,
kuma amintacce, ba zan qara komai a cikin abin
da zan isar muku daga gare shi, kuma ba zan rage
komai ba". (144) "Don haka ku ji tsoron Allah ta
hanyar kamanta umarninsa, da nesantar haninsa,
kuma ku yi min biyayya cikin abin da na yi muku
umarni da shi, da abin da nake muku hani a kai".
(145) Kuma ba na neman wani lada a wurinku, a
kan abin da nake isar muku daga Ubangijina,
lada na ba ya wajen kowa sai Allah, Ubangijin
talikai baki xaya, ba a wajen waninsa ba. (146) Shin
kuna son a bar ku ne a cikin abin da kuke ciki, na
alherai da ni'imomi, cikin aminci ba tare da wani
tsoro ba?. (147) A cikin gonaki da idanuwan ruwa
masu gudana.
(148) Da shuke-shuke da dabinai masu 'ya'ya tausasa nunannu?. (149) Kuma kuna fasa duwatsu, domin ku gina
gidajen da zaku zauna a ciki, wanda kun qware a wajen fasa waxannan duwatsun. (150) Don haka ku ji tsoron Allah
ta hanyar kamanta umarninsa da nesantar haninsa, kuma ku yi min biyayya cikin abin da na yi muku umarni da
shi, da abin da nake muku hani a kai. (151) Kuma kar ku bi umarnin masu yi wa kansu varna, ta hanyar aikata savo.
(152) Waxanda suke barna a bayan qasa, da abin da suke yaxawa a cikinta na savo, kuma ba sa gyara kawunansu da
lizimtar biyayya ga Allah. (153) Sai Mutanen sa suka ce masa: "Kai fa kana cikin waxanda aka yi wa tsafi da yawa, har
tsafin yayi galaba a kan hankulansu, ya tafiyar da su". (154) "Kai ba kowa ba ne, face mutum ne irin mu, baka da wani
fifiko a kanmu ballantana ka zama Manzo, don haka ka kawo mana wani dalili da zai nuna cewa kai Manzo ne, in
kana da gaskiya cikin abin da kake da'awarsa, na cewa kai Manzo ne". (155) Annabi Salihu ya ce musu, - bayan Allah
ya ba shi alama, wadda ita ce taguwar da Allah ya fitar da ita daga dutse – don haka ya ce da su: "Wannan Taguwa
ce ana ganinta ana kuma iya tava ta, tana da rabo daga wannan ruwa, ku ma kuna da naku rabon sananne, ba zata
sha ruwa a ranar da yake rabon ku ne ba, ku ma ba zaku sha ruwa a ranar da yake rabonta ne ba". (156) "Kuma kar
ku tava ta da wani abin da zai munana mata, na suka, ko duka, sai azabar Allah ta same ku a dalilin hakan, Allah ya
halaka ku da ita a wani yini mai girma, saboda abin da yake cikinsa na bala'in da zai sauka a kanku". (157) Sai suka
haxu akan su soke ta, sai wanda ya fi kowa rashin arziki ya soke ta, sai suka wayi gari suna masu nadama a kan
abin da suka aikata, yayin da suka san babu makawa azaba zata sauka a kansu. Sai dai nadama bata amfani yayin
da aka ga azaba. (158) Sai azabar da aka yi musu alqawari ta same su, ita ce girgizar qasa da tsawa. Haqiqa a cikin
wannan abin da aka ambata na qissar Annabi Salihu (A.S) da mutanensa akwai abin lura ga masu la'akari, amma
mafi yawansu basu kasance masu imani ba. (159) Kuma lallai Ubangijinka – Ya kai wannan Manzo- shi ne Mabuwayi,
mai xaukan fansa a kan abokan gabarsa, kuma mai jin qai ga wanda ya tuba daga cikin bayinsa.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Ci gaban samun ni'ima duk da kafircin da ake aikatawa, talala ne zuwa ga halaka. 2 - Ana tunawa bawa ni'imomin Allah don fatan ya koma zuwa ga Allah, ya yi imani. 3 - Zunubai su ne sababin varna a bayan qasa.**

كَذَّبَتْ قَوْمُ لُوطٍ ٱلْمُرْسَلِينَ ١٦٠ إِذْ قَالَ لَهُمْ أَخُوهُمْ لُوطٌ أَلَا تَتَّقُونَ
١٦١ إِنِّي لَكُمْ رَسُولٌ أَمِينٌ ١٦٢ فَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ وَأَطِيعُونِ ١٦٣ وَمَآ
أَسْـَٔلُكُمْ عَلَيْهِ مِنْ أَجْرٍ إِنْ أَجْرِيَ إِلَّا عَلَىٰ رَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ١٦٤
أَتَأْتُونَ ٱلذُّكْرَانَ مِنَ ٱلْعَٰلَمِينَ ١٦٥ وَتَذَرُونَ مَا خَلَقَ لَكُمْ رَبُّكُم
مِّنْ أَزْوَٰجِكُم بَلْ أَنتُمْ قَوْمٌ عَادُونَ ١٦٦ قَالُوا۟ لَئِن لَّمْ تَنتَهِ يَٰلُوطُ
لَتَكُونَنَّ مِنَ ٱلْمُخْرَجِينَ ١٦٧ قَالَ إِنِّي لِعَمَلِكُم مِّنَ ٱلْقَالِينَ ١٦٨
رَبِّ نَجِّنِي وَأَهْلِي مِمَّا يَعْمَلُونَ ١٦٩ فَنَجَّيْنَٰهُ وَأَهْلَهُۥٓ أَجْمَعِينَ ١٧٠
إِلَّا عَجُوزًا فِي ٱلْغَٰبِرِينَ ١٧١ ثُمَّ دَمَّرْنَا ٱلْءَاخَرِينَ ١٧٢ وَأَمْطَرْنَا عَلَيْهِم
مَّطَرًا فَسَآءَ مَطَرُ ٱلْمُنذَرِينَ ١٧٣ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَءَايَةً وَمَا كَانَ أَكْثَرُهُم
مُّؤْمِنِينَ ١٧٤ وَإِنَّ رَبَّكَ لَهُوَ ٱلْعَزِيزُ ٱلرَّحِيمُ ١٧٥ كَذَّبَ أَصْحَٰبُ
لْـَٔيْكَةِ ٱلْمُرْسَلِينَ ١٧٦ إِذْ قَالَ لَهُمْ شُعَيْبٌ أَلَا تَتَّقُونَ ١٧٧ إِنِّي لَكُمْ
رَسُولٌ أَمِينٌ ١٧٨ فَٱتَّقُوا۟ ٱللَّهَ وَأَطِيعُونِ ١٧٩ وَمَآ أَسْـَٔلُكُمْ عَلَيْهِ
مِنْ أَجْرٍ إِنْ أَجْرِيَ إِلَّا عَلَىٰ رَبِّ ٱلْعَٰلَمِينَ ١٨٠ ۞ أَوْفُوا۟ ٱلْكَيْلَ وَلَا الحزب ٣٨
تَكُونُوا۟ مِنَ ٱلْمُخْسِرِينَ ١٨١ وَزِنُوا۟ بِٱلْقِسْطَاسِ ٱلْمُسْتَقِيمِ ١٨٢
وَلَا تَبْخَسُوا۟ ٱلنَّاسَ أَشْيَآءَهُمْ وَلَا تَعْثَوْا۟ فِي ٱلْأَرْضِ مُفْسِدِينَ ١٨٣



**(160) Mutanen Annabi Luxu sun qaryata Manzanni,
saboda sun qaryata Manzonsu Annabi Luxu
(A.S). (161) Yayin da xan uwansu cikin dangantaka,
Annabi Luxu ya ce musu: "Shi ba zaku ji tsoron
Allah ba, ku daina yi masa shirka don tsoronsa?!".
(162) Ni Manzo ne zuwa gare ku, Allah ne ya aiko
ni zuwa gare ku, kuma ni Amintacce ne cikin abin
da na ke isar muku daga gare shi, ba zan yi mishi
qari ba, ba zan yi ragi ba". (163) Don haka ku ji
tsoron Allah, ta hanyar kamanta umarninsa da
nesantar haninsa, kuma ku yi mini biyayya cikin
abin da nake muku umarni da shi, da abin da
nake hane ku a kai. (164) Kuma bana neman wani
lada daga wurinku a kan abin da nake isar muku,
daga wurin Ubangijina, Ladana ba a wurin kowa
yake ba face a wurin Allah, Ubangijin talikai baki
xaya, ba a wurin waninsa ba. (165) Yanzu kuna
zakke wa maza cikin mutane ta dubarar su?!.
(166) Kuma ku qyale abin da Allah ya halitta muku,
don ku biya buqatarku na farjin matekun ku?!
Kai! ku mutane ne masu qetare iyakokin Allah, ta
hanyar wannan baqon abu, mummuna!. (167) Sai
Mutanensa suka ce masa: "Kai Luxu tabbas idan
baka kame daga hana mu wannan aikin ba, baka
daina yi mana inkari ba, to lallai zaka kasance, kai
da duk wanda yake tare da kai, cikin waxanda za
a kore su, a fitar da su daga wannan gari namu".
(168) Sai Annabi Luxu ya ce musu: "Tabbas ni
dangane da wannan aiki da kuke yi, ina cikin
masu qyamarsa da fushi da shi". (169) Sai ya roqi
Ubangijinsa ya ce: "Ya Ubangijina ka kuvutar da
ni da iyalina daga abin da zai samu waxannan,
saboda abin da suka kasance suna aikatawa, na mummunan aiki". (170) Sai muka amsa roqonsa, muka kuvutar da
shi da iyalansa gaba xayansu". (171) Ban da matarsa, don ta kasance kafira, sai ta zama cikin waxanda aka yi gaba
da su, aka halakar da su. (172) Bayan Annabi Luxu da iyalansa sun fice daga qarin (Sadum), sai muka halakar da
mutanensa da suka rage, halaka mafi tsanani. (173) Muka saukar musu da duwatsu daga sama, kamar yadda ake
saukar da ruwan sama, wannan ruwan saman da aka saukar wa waxannan da Annabi Luxu ya kasance yana musu
gargaxi, yana musu kashedi da azabar Allah in suka zarce akan abin da suke a kai, na mummunan aiki, ya yi muni.
(174) Lallai cikin wannan abin da aka ambata, na azabar da ta sauka a kan mutanen Annabi Luxu, a dalilin aikata
alfasha, akwai abin lura ga masu la'akari, amma mafi yawansu basu kasance masu imani ba. (175) Kuma lallai
Ubangijinka – Ya kai wannan Manzo- shi ne Mabuwayi, mai xaukan fansa a kan abokan gabarsa, kuma mai jin
qai ga wanda ya tuba daga cikin bayinsa. (176) Mutanen garin nan mai bishiyoyi da yawa, waxanda suke luf-luf, kusa
da garin madyana sun qaryata Manzanni, yayin da suka qaryata Manzonsu Annabi Shu'aibu (A.S). (177) Yayin da
Annabinsu, ya ce musu: "Shi ba zaku ji tsoron Allah ba, ku daina yi masa shirka ku ji tsoronsa?!". (178) "Haqiqa ni
Manzo ne zuwa gare ku, Allah ne ya aiko ni wurinku, kuma ni amintacce ne cikin abin da na ke isar muku daga
gare shi, ba zan yi mishi qari ba, kuma ba zan yi ragi ba". (179) Don haka ku ji tsoron Allah, ta hanyar kamanta
Umarninsa da nesantar haninsa, kuma ku yi mini biyayya cikin abin da nake muku umarni da shi, da abin da
na haneku a kai". (180) Kuma bana neman wani lada daga wurinku a kan abin da nake isar muku daga wurin
Ubangijina, ladana baya kan kowa yake face Allah Ubangijin talikai baki xaya, ba a wajen waninsa. (181) Ku cika
wa mutane mudu yayin da kuka yi cikini da su, kar ku kasance cikin waxanda suke tauye mudu idan sun yi hulxar
cinikayya da mutane. (182) Kuma yayin da zaku yi wa mutane, ku yi da mau'uni daidaitacce. (183) Kuma kar ku tauye
wa mutane haqqoqinsu, kuma kar ku yawaita varna a bayan qasa, ta hanya aikata savo.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Luwaxi fita ne daga tsarin halittar xan
Adam, kuma abin qi ne mai girma . 2 - Yana daga cikin jarrabawa ga mai kira zuwa ga Allah, mutanen gidansa
su zama cikin ma'abota kafirci ko savo. 3 - Alaqa ta zama qasa xaya idan bata haxu da imani ba, ba zata amfani
ma'abocinta ba idan azaba ta sauka. 4 - Wajabcin cika mudu da haramcin tauye shi.**

وَٱتَّقُواْ ٱلَّذِي خَلَقَكُمۡ وَٱلۡجِبِلَّةَ ٱلۡأَوَّلِينَ ١٨٤ قَالُوٓاْ إِنَّمَآ أَنتَ مِنَ
ٱلۡمُسَحَّرِينَ ١٨٥ وَمَآ أَنتَ إِلَّا بَشَرٞ مِّثۡلُنَا وَإِن نَّظُنُّكَ لَمِنَ
ٱلۡكَٰذِبِينَ ١٨٦ فَأَسۡقِطۡ عَلَيۡنَا كِسَفٗا مِّنَ ٱلسَّمَآءِ إِن كُنتَ
مِنَ ٱلصَّٰدِقِينَ ١٨٧ قَالَ رَبِّيٓ أَعۡلَمُ بِمَا تَعۡمَلُونَ ١٨٨ فَكَذَّبُوهُ
فَأَخَذَهُمۡ عَذَابُ يَوۡمِ ٱلظُّلَّةِۚ إِنَّهُۥ كَانَ عَذَابَ يَوۡمٍ عَظِيمٍ ١٨٩
إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَأٓيَةٗۖ وَمَا كَانَ أَكۡثَرُهُم مُّؤۡمِنِينَ ١٩٠ وَإِنَّ رَبَّكَ
لَهُوَ ٱلۡعَزِيزُ ٱلرَّحِيمُ ١٩١ وَإِنَّهُۥ لَتَنزِيلُ رَبِّ ٱلۡعَٰلَمِينَ ١٩٢ نَزَلَ بِهِ
ٱلرُّوحُ ٱلۡأَمِينُ ١٩٣ عَلَىٰ قَلۡبِكَ لِتَكُونَ مِنَ ٱلۡمُنذِرِينَ ١٩٤ بِلِسَانٍ
عَرَبِيّٖ مُّبِينٖ ١٩٥ وَإِنَّهُۥ لَفِي زُبُرِ ٱلۡأَوَّلِينَ ١٩٦ أَوَلَمۡ يَكُن لَّهُمۡ ءَايَةً
أَن يَعۡلَمَهُۥ عُلَمَٰٓؤُاْ بَنِيٓ إِسۡرَٰٓءِيلَ ١٩٧ وَلَوۡ نَزَّلۡنَٰهُ عَلَىٰ بَعۡضِ ٱلۡأَعۡجَمِينَ
١٩٨ فَقَرَأَهُۥ عَلَيۡهِم مَّا كَانُواْ بِهِۦ مُؤۡمِنِينَ ١٩٩ كَذَٰلِكَ سَلَكۡنَٰهُ
فِي قُلُوبِ ٱلۡمُجۡرِمِينَ ٢٠٠ لَا يُؤۡمِنُونَ بِهِۦ حَتَّىٰ يَرَوُاْ ٱلۡعَذَابَ
ٱلۡأَلِيمَ ٢٠١ فَيَأۡتِيَهُم بَغۡتَةٗ وَهُمۡ لَا يَشۡعُرُونَ ٢٠٢ فَيَقُولُواْ
هَلۡ نَحۡنُ مُنظَرُونَ ٢٠٣ أَفَبِعَذَابِنَا يَسۡتَعۡجِلُونَ ٢٠٤ أَفَرَءَيۡتَ
إِن مَّتَّعۡنَٰهُمۡ سِنِينَ ٢٠٥ ثُمَّ جَآءَهُم مَّا كَانُواْ يُوعَدُونَ ٢٠٦



**(184) Kuma ku ji tsoron wanda ya halicce ku, ya halicci al'ummun da suke gabace ku, ta hanyar jin tsoronsa, kar ya saukar da uqubansa a kanku. (185) Sai mutanen Annabi Shu'aibu suka ce wa Annabi Shu'aibu: "Kai kana cikin waxanda sihiri ya kama su, har ya yi galaba a kan hankalinka, ya tafiyar da shi". (186) Kuma kai ba kowa ba ne face mutum irin mu, baka da wani fifiko a kanmu, to ta yaya zaka zama manzo? Ba ma zatonka face maqaryaci ne, cikin abin da kake iqrari na cewa kai manzo ne". (187) Ka jeho mana wani vangare na sama a kanmu (Ya halaka mu) in ka kasance mai gaskiya cikin abin da kake iqrari. (188) Sai Annabi Shu'aib ya ce,: "Ubangijina shi ya fi kowa sanin abin da kuke aikatawa na shirka da savo, babu abin da yake vuya a gare shi, na ayyukan ku". (189) Sai suka ci gaba da qaryata shi. Sai wata azaba mai girma ta shafe su, ta yadda wani hadari ya yi lulluve su bayan wani yini mai tsananin zafi, ya yi musu ruwan wuta ta qone su,. Lallai ranar halakar da su ta kasance rana ce mai tsananin ban tsoro. (190) Lallai a cikin wannan abin da akan ambata na halakar da mutanen Annabi Shu'ibu, akwai abin lura ga masu la'akari, amma mafi yawansu ba su kasance masu imani ba. (191) Kuma Haqiqa Ubangijinka – Ya kai wannan Manzo- shi ne Mabuwayi, mai xaukan fansa akan abokan gabarsa, kuma mai jin qai ga wanda ya tuba cikin bayinsa. (192) Haqiqa wannan Alqur'anin da aka saukar wa Annabi Muhammad (S.A.W) sauqaqke ne daga Ubangijin halitta. (193) Mala'ika Jibrilu (A.S) wanda yake amintacce shi ne ya sauko da shi. (194) Ya saukar da shi a cikin zuciyarka – Ya kai wannan manzo- don ka kasance cikin Manzanni, waxanda suke yi wa mutane gargaxi da tsoratar da su daga azabar Allah. (195) Ya saukar da shi ne da harshen larabci bayyananne. (196) Haqiqa wannan Alqur'anin an ambace shi a cikin littafan mutanen farko, saboda littafan da aka saukar daga sama waxanda suka gabace shi, sun yi albishir da shi. (197) Yanzu ba zai zama alamar dake nuna gaskiyar ka ba, a wurin waxannan masu qaryatawar kasancewar malaman Bani Isra'ila, irin su Abdullah bin Salam, sun san haqiqanin abin da ya sauka a gare ka ba? (198) Da a ce mun saukar da wannan Alqur'anin ga wasu waxanda ba larabawa ba, waxanda ba sa magana da yaren larabci. (199) Sai ya karanta musu, to da basu yi imani ba, domin za su ce,: "Bama gane shi" Don haka su godewa Allah da ya saukar da shi da harshensu.**
**(200) Kamar haka muka cusa qaryata wa da kafirci a zukatan masu laifi.**
**(201) Ba za su canza daga abin da suke kai na kafirci ba, kuma ba zasu yi imani ba, har sai sun ga azaba mai raxaxi.**
**(202) Wannan Azabar ta zo musu kwatsam, basu da masaniyar zuwanta, sai ta yi musu bazata.**
**(203) Sai su ce, a yayin da azaba take sauko musu ba shiri, saboda da tsananin baqin ciki: "Shin ina ma da za a yi mana jinkiri, sai tuba zuwa ga Allah?!". (204) Shi dangane da azabrmu ne waxannan kafirai suke gaggawa, har suke cewa: "Ba zamu yi imani da kai ba, har sai ka sa wani vangare na sama ya faxo a kanmu, kamar yadda kake riyawa hakan zai faru?". (205) Ka bani labari – Ya kai wannan Manzo- in har muka jiyar da waxannan kafirai masu bijirewa imani da abin da ka zo da shi, jin daxin ni'imomi na wani lokaci mai tsawo.**
**(206) Sannan sai abin da ake musu alqawari na azaba ya zo musu, bayan wannan lokacin da suka kwashe suna jin daxin waxannan ni'imomin.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Duk lokacin da Musulmi ya qara zurfi cikin sanin harshen larabci, to zai qara samun ikon fahimtar Alqur'ani.**
**2 - Kafa hujja a kan Mushirikai da abin da ke wurin masu adalci cikin ma'abota Littafi (Ahlul Kitab) na tabbatar da cewa Alqur'ani daga wurin Allah yake. 3 - Abin da yake samuwa ga kafirai na jin daxi talala ne ba girmamawa ba ne.**